Scanned and Regged by
Abdalla Uba Adamu for
Foundation for Hausa Performing Arts (fohapa.com)

Muhammad Sani Gwarzo

IDON MATAMBAYI

1933 Literary Competition Winner



IDON MATAMBAYI

IDON Matambayi mutum ne wanda Allah ya ba shi yawan hankali da natsuwa. Ga shi kyakkyawa, idanu daradara da wuya santalele. Allah ya ba shi yawan sa'a a kan mutane, amma bai ba shi sa'a ba a kan abin da ya samu daga wurin mutanen. Ga shi ƙaƙƙarfa, kan ya sa hannu ya yi wa ko wane irin mutum ƙulli, im mutumin nan bai mutu ba, ya sha wuya. Ban da wannan kuma Allah ya ba shi gudu da vawa kamar zomo. Amma bai tashi ƙasaita ba sai da ya hadu da mutane guda biyu, su ne 'Dauke da Kwace.

Da ya soma datawa sai ya shiga 'yan ɗauke-ɗauke tun a gidansu, har ya kai yi wa maƙwabta. Maƙwabtan kuwa ba su taba yi masa kome ba sabo da kunyar ubansa.

Ana nan ran nan ubansa ya ji labarin abin da ya ke yi, sai ya sa yaronsa ya je ya kirawo shi. Da zuwansa ubansa ya ce, "Tattara 'yan kayanka duka, yau ka bar mini gidana. Na yarda ka, kada wata rana ka je ka jawo mini abin da ya fi ƙarfina."

Da jin haka, da ma abin da ya ke so ke nan, sai ya tashi bai ce kome ba. Da tashinsa daga nan ya tafi wurin wani boka ya ce da shi, "Ka ji ka ji yadda muka yi da babana. Ina so don Allah ka taimake ni ka ba ni maganin tsoro da na ƙarfin zuciya."

Boka ya kada baki ya ce, "Haba, dan saurayi, ai sabo da kyaunka duk abin da ka ce in yi ma, na yi maka shi, sai dai wanda ya fi ƙarfina. Wannan abu an gama. Shigo nan!" Suka shiga wata 'ya taska matsattsa. Boka ya ce, "Zauna nan, ina zuwa y nzu yanzun nan.


Idon Matambayi ya zauna, boka ya fita ya bar shi ana jiransa. Bai dade da fita ba sai Idon Matambayi ya ga daki ya yi duhu sai ka ce da dare. Aka jima can sai ga ji wani abu ya faso daga bisan daki sakasaka, bai dai kula ba balle ya ji tsoro. Daga nan sai ya ji bif a kusa da shi a gabansa, kamar wani katon dutse aka jefo ya fado. Shiru, shiru, shiru, ba motsi. Daga nan sai jikin Idon Matambayi ya dau rawa farfar, tsoro ya kama shi. Yana cikin wannan hali sai ya ga wayau, jikin duk ya haska da haske, ya cika da kanshin turare. Idon Matambayi ya duba nan ya duba can, ya ga abin da ya fado kamar dutse na dazu bai gani ba. Yana cikin haka sai ga boka, ya ce, "To, na dawo."

"Sannu da zuwa. Kai, boka, dakin nan akwai abin tsoro da yawa, ka ji ka ji abin da na ji da wanda na gani sayan ka fita." Boka ya ce, "To, madalla ! Da ka ji bubuwan nan me ka yi, ko me ka ce?"

"Ban ce kome ba, sai na zuba wa sarautar Allah ido."

Boka ya ce, "Babu wani maganin tsoro irin in ka yi niyyar yin abu kada ka fasa shi sabo da wuyarsa ko tsoronsa. Kama hanya ka tafi, ka yi abin da ka ga dama, tsoro ya kare a wurinka." Idon Matambayi ya ce, "Sai wata rana." "To, da alheri."

Da fitar Idon Matambayi gidan boka ya tafi tirantiran bai dire ba sai kasuwa, har inda aka zuba kudin cinikin hajja a kan tabarma, ya lababo kamar wanda zai sayi wani turmin sanda. Wuf! Ya duntse tsabar kudi sule sule ya sheka a guje, ana binsa ana ku tare ku tare. Shi kuma yana kutsawa cikin mutane yana cewa ku tare ku tare, don kada a kama shi. Da dai ya sami fam fili ya rankada da gudu, ya yi maza ya fada wani gida, daga nan kuma ya fada wani. Ya yi ta yin haka har kafin a jima an rasa inda ya ke takamaimai, aka gaji aka kyale shi.



Ran nan bai kwana garin nan ba sai wani ƙauye, ya tafi bakin kasuwa ya sayi abinci, ya ci ya ƙoshi, ya tafi wata rumfa ya kwana. Da gari ya waye ya sayi abinci ya ci, ya tashi, ya kama hanya ya yi ta tafiya har rana ta soma zafi.

Ya hangi wata itaciya mai inuwa liflif, ya tafi gindinta ya zauna. Ashe bai sani ba cewa hanyan nan ta 'yam fashi ce, tun ba lokacin da rana ta take a tsaka ba. Yana nan zaune sai ya ga kibiya ta dira a gabansa dik. Ya duba gabas, ya duba arewa, ya duba kudu, ya duba yamma, bai ga kowa ba. Ya ɗaga kansa dai bisa, sai ya ga mutane guda biyu a kan wani reshe mai 'yar duhuwa, ko wanne da kwari a rataye, da baka da kibiya a ɗane. Ya dube su ya yi murmushi ya ce, "Ashe ku ne ma kuka harbo ni ? In dukiya ku ke so, ku sauko ku zo nan, ga ta."

Da jin haka mutanen nan suka sauko. Da saukarsu Idon Matambayi ya dubi ɗayansu ya buga masa ƙulli a ciki, ya faɗi warwas, sumamme. Dayan da ganin haka sai ya kai masa harbi, ya same shi a cinya, kibiya ta kafe (Allah ya sa ba ta da ɗafi). Idon Matambayi ya sa hannu ya cire kibiyar. Da ganin jan halin nan nasa, sai Barawon ya ce, "Zo mu je!" Suka yi ta gudu, suka yi ta gudu, Idon Matambayi na biye, har Barawo ya gaji ya tsaya don kansa. Da tsayawarsa sai ya ce "Ka yi mini sutura, don Allah kada ka kashe ni, na ga ɗanuwana wanda muka haɗa a kwanc

Idon Matambayi ya yarda, suka koma.

Ya Sami Abokai

DAM fashin da aka bari a kwance jimawa kaɗan ya farfaɗo, ya duba, ya sake dubawa, bai ga kowa ba har azahar ta yi. Can bayan azahar kaɗan ya duba gabas, sai ya hango mutane biyu suna tahowa wajensa, ɗaya a gaba, ɗaya a baya. Suna tahowa yana dubansu har suka yi kusa da shi, bai gane ɗanuwansa ba ne tare da Idon Matambayi. Da zuwansu sai ya tada kansa ya ce, "Ashe da rabon za mu sake ganawa, Ɗauke?"

Ɗauke ya ce, "To, ga mu dai, Kwace."

Da jin sunayen nan, Ɗauke da Kwace, Idon Matambayi ya ce a zuciyarsa, "Wallahi, ba na kashe mutanen nan sai na ji dalilin da ya sa su ke da sunayen nan dabam da na mutane." Kuma ya ce, "Bari in duba ko garin gudun nan na zubar da kuɗina." Da dubawarsa sai kuɗi suka ce ɗebarmu inda ka ajiye mu. Ya yi salati, ya sanar da Ubangiji.

Mutanen nan guda biyu suka ce, "Yaya muka ji kana [illegible] da sallallami?"

Idon Matambayi ya ce, "Ku bari, ai na zubar da kuɗina masu yawa."

Suka ce, "Allah ya tsananta rabo."

Ya ce, "Amin!"

Ɗauke ya ce, "To, ina dabara? Za ka kashe mu ne, ko za ka bar mu?"

Idon Matambayi ya yi shiru kaɗan, bai ce kome ba. Aka jima ya ce, "Ni ba zan kashe ku ba sai kun faɗa mini dalilin da sunayenku su ke dabam da na sauran mutane." Ya ɗaga kansa ya ce, "Kai Kwace, me ya sa aka sa maka sunan nan?"

Kwace jikinsa na rawa, ya ce, "Ba dalilin da ya sa a ke ce da ni Kwace sai don ni kan gamu da mutum da

kayansa, in ƙwace masa, in tsere da kayan a guje fartai."

Idon Matambayi ya yi dariya ya ce, "To, na ji naka. Kai kuwa fa, Ɗauke ?"

Ɗauke ya kada baki ya ce, "Ni Ɗauke, abin da ya sa kowa ya san ni da sunan nan domin ko ina ɗan Adam ya sa kayansa na iya in ɗauke shi, ko da ƙarfi, ko da wayo."

Idon Matambayi ya yi shiru yana zancen zuci yana cewa, "Allah ya haɗa ni da abokan zama waɗanda za su taimake ni a kan al'amarin sata in sami dukiya mai yawa, don haka ban ga amfanin in kashe su ba."

Sai ya ce musu, "Kun gani ni sunana Idon Matambayi, ba ni da wani ciniki a duniyan nan sai sata kamarku, sabo da haka ba zan kashe ku ba, amma ina so mu zauna tare da ku, mu riƙa sata gaba ɗaya."

Suka ce, "Mun gode ! Mun gode ! Allah kuwa ya ɗora mu bisa kan masu abu, mu tsiyata mai dukiya, mu sabarta mahukunci, mu talauta talaka. Yanzu sai mu tafi ka ga gidammu, domin yanzu ka ga almuru ta kusa."

Suka kama hanya suna tafiya, Kwace na gaba, Idon Matambayi na tsaka, Ɗauke kuwa na baya. Suka yi ta tafiya cikin duhu, su ɗaɗa wannan kwazazzabo, su yi karo da wannan marmaya, ba wanda ya ke ce wa kowa uffan. Idon Matambayi kuwa yana ta tunanin ɓatan kuɗinsa. Har suka isa gidansu tsakanin duwatsu guda biyu dogwaye. Da isarsu Kwace ya shiga, ya ce wa Idon Matambayi, "Bismilla." Idon Matambayi ya shiga, Ɗauke na biye da shi a baya.

Da shigarsu sai Idon Matambayi ya duba ya ga ɗan gidan nasu yana cike da ni'ima mai yawa. Ga wani ɗaki mai bangon dutse, cikinsa kuma akwai wani babban kogon dutse inda su ke ajiye kayan da suka sato. Kwace ya ce masa, "Duba can." Ya nuna wani wuri da

hannu a cikin ɗakin. Ya duba ya ga nan ga soyayyen nama da ƙyafaffe, da abinci iri iri na daɗi. A wani waje kuwa babu kome sai kibiyoyi da kwarurruka iri iri da masu, da takubba, da wuƙaƙe, suna walƙiya walwal. Da ya ga haka ya ce a zuciyarsa, "Yau Allah ya kawo ni wurin halaka a sarari, da dai na san mutanen nan haka su ke, da tun a can na kashe su. Ga kuɗina sun zube, ga shi kuma na kawo kaina wurin halaka. Da in ƙyale su mana ! Ga shi zam mutu ba kuɗi ba girma, na yi wa duniya zuwan zomo kasuwa ke nan. Amma Allah na nan, domin ni dai alheri na yi musu."

Amma dukan abin da ya yi tsammani game da mutanen nan bai faru ba, sai alheri. Aka jima kaɗan suka shiga wani ɗan kwalogo a ɗakin nan suka kunna fitila, kowa ya zauna. Da zamansu sai Ɗauke ya ce, "Shin ni ne kaɗai na ke jin zafin raunin nan, ko ƙarfin hali kuka fi ni ?"

Da jin haka Idon Matambayi ya yi farat da baka ya sako wani labari, don kada su tuna abubuwan da ya yi musu. Ya yi maza ya ce, "Shin yaya sunan gidan nan naku ?" Yana shashatar da zancen rauni, ko da ya ke shi ma yana jin zafin nasa ƙwarai.

Kwace ya ce, "Sunansa Sauke-mu-raba, watau duk abin da ya shigo ɗakin nan, ko na sata ne, ko ba na sata ba ne, lalle a raba shi daidai wa daida."

Kogon Dutse Ne Ɗakin Barayi

CAN kusan ɗare tsaka Ɗauke ya tashi, kamar wanda za shi bawali, ya ɗauko nama soyayye suka ci suka ƙoshi, ya ɗauko taba sigari gwangwan ɗaya, ya sa hannu ya buɗe ya juye, suka yi ta sha, suna zance har wani lokaci. Aka jima kaɗan suka yi shirin kwanciya. Ɗauke ya ɗauko barguna da matasan kai ya shimfiɗa wa Idon Matambayi, suka kwanta suka yi ta barci.

Da gari ya waye Idon Matambayi ya ga gidan nan da kyar a ke ganin rana. Suka tashi suka wawwanke fuskokinsu, suka koma suka zauna. Da hantsi ya soma zafi Dauke ya kawo musu 'yar waina haɗe da nakiya suka ci. Wajen kusan azahar Kwace ya ce, "Ina dabarar abin da za mu yi yau ? Mu tafi ne gaba ɗaya mu uku wurin da mutane su ke yawan wucewa, mu laɓe har Allah ya jeho mana da rabommu ?"

Aka jima ba wanda ya tanka wa Kwace. Sa'an nan Idon Matambayi ya ce, "To, ba abin da kuka gani zai fisshe mu za mu yi ba ?"

Kwace ya ce, "Haka ne fa."

Aka haɗa shawara Kwace da Idon Matambayi su tafi hanyar fatake masu wucewa, su laɓe har Allah ya kawo rabonsu. Dauke kuwa ya zauna a gida sai azahar ta yi ya tafi Kafi, wani gari ne kusa da Sauke-mu-raba, ya sayo abincin da za su ci da dare, kuma a Kafi ɗin ya duba a hankali ko Allah ya sa ya ga wani gidan attajiri wanda za su kai wa hari da dare. Suka haɗu a kan haka, shawara ta zauna.

Idon Matambayi da Kwace suka warwasa wuƙaƙensu, suka ɗau kibau da bakunna kamar maharba, suka fita. Suka yi ta tafiya har suka isa wani ɗan rafi a gefen wata babbar hanya. Kwace ya ce, "Wurin nan za mu laɓe." Ya nuna wani wuri a bakin rafi.

Idon Matambayi ya ce, "Sabo da me ?"

Kwace ya ce, "Haba, kada ka yi mini yankan hanzari mana wanda ya hana Barka laiata da 'yarsa. Ka ga wurin nan yau kusan shekararmu guda ke nan mu ke fashi, ba ranar da kuwa ba mu samun wani abu. Gama sabo da sanin ba ma rabo da nan har idan mun ce wa matafiyi ya ba mu abu kaza, maza-maza, ya kan ba mu, jikinsa na rawa. Kai Idon Matambayi, wurin nan sa'a gare shi mai yawa !"

Idon Matambayi ya ce, "Wassalam ! Ai ko ba sa'a ma iya karɓar abu a hannun mutum, ko wane ne shi cikin ko wane hali."

Kwace ya ce, "A'a, Idon Matambayi, kada ka ce haka, kai dai Allah ya taimake mu."

Suka matsa daga wurin da su ke, suka sami wata 'yar duhuwa suka tsugunguna, kowa da bakansa da kibiya a ɗane. Suka daɗe ba su ga ko kare ya gifta hanyan nan ba, balle mutum. Kwace ya ce, "Bari in hau doguwar itaciyar can, ko zan hango waɗansu mutane suna zuwa."

Idon Matambayi ya ce, "To."

Kwace ya hau itaciyar, ya hanga ko ina bai ga kowa ba. Aka jima ya sake hangawa, sai ya hango wani babban ayari yana tafe da jakuna ɗauke da kaya niƙiniƙi. Da ganin haka ya yi maza ya sauko, ya koma wurin Idon Matambayi, ya ce, "Wallahi, yau sai mun ga abin da ya cire wa buzu naɗi, da mu da mutanen nan masu tahowa."

Idon Matambayi ya ce, "Waɗanne irin mutane ne ?"

Kwace ya ce, "Haba, bari ai yau kakarmu ta yanke saƙa ! Ba ka ga yawan kayan da jakunan mutanen nan su ke ɗauke da su ba !"

Idon Matambayi ya ce, "Abin da za mu fara yi, da sun iso sai in yi ɓut im fito in ce, "Ku kawo kuɗin hanya !" In sun ƙi sa'an nan mu karɓa da ƙarfi. Ka bar ni da su da farko, sai ka ga suna neman su fi ƙarfina, sa'an nan ka fito ka taimake ni."

Kwace ya ce, "Haka za a yi ! Balle ga shi kuwa maza na kan ƙwace abu a hannun mutum."

Suna cikin haka sai suka ji, "Kai !" Idon Matambayi ya ce, "A'a ! Tun ba su gan ni ba su ke cewa 'Kai !' Lalle mutanen nan da tsoro."



Kwace ya ƙyalƙyale da dariya ya ce, "Ai ba da mu su ke ba, da jakunansu su ke."

Idon Matambayi ya fito ya tsaya. Bai daɗe ba sai suka iso. Da isarsu suka ga mutum a tsaye ƙiƙam da kwari da baka a ɗane. Wani a cikin ayarin nan ya ce, "Da ma na sami labarin dawan nan a kan fashi, yau kam sai Allah mu da wannan mutum !"

Kafin su iso wurinsa Idon Matambayi ya murtuke fuskarsa ya zazzare idanu don su tsorata. Da isowarsu wurinsa ya ce da su, "Kai ! Ku kawo kuɗin hanya, ko kuwa in halaka ku duk yanzu ! Kun ji ko ba ku ji ba ?"

Mutane duk suka yi shiru, kowa jikinsa yana rawa, sai wani matsoraci a cikinsu ya ce, "Mun ji. To, nawa za mu ba ka ?"

Yayin da duk a ke wannan abu Kwace yana laɓe yana jin abin da su ke yi. Su kuwa ba su san yana nan ba.

Idon Matambayi ya ce, "Duk kayan jakunanku za ku sauke ku tafi."

Suka ce, "To."

Suka yi ta sauke kaya, kowa yana kora jakinsa yana tafiyarsa sai wani mai taurin zuciya a cikinsu ya ce, "Wallahi, ba na sauke kayana sai mun taɓa 'yar daga da mutumin nan. Ni mutum ne, shi kuma mutum ne kamata."

'Yanuwansa suka ce, "Kayanka ne, ranka ne, in ka fi son kayanka da ranka ka tsaya ku yi 'yar dagar, mu dai ka ga tafiyarmu sai wata rana, ko kuma watakila sai gobe kiyama ta yi." Suka kama hanya suka yi tafiyarsu suka bar shi.

Da jin haka Idon Matambayi ya tattakura ya tsilla wa mutumin nan kibiya a ciki, ta taɓa cikin ta faɗi a ƙasa a lauye. Ya koma da baya ya sake harbo wata kibiyar. Wannan ko jikin mutumin nan ba ta taɓa ba, ta faɗi gabansa. Idon Matambayi ya yi mamaki da abin da mutumin nan ya yi. Ya zaro wuƙa ya daɓa masa ta karye, wuƙaƙensa duk ran nan suka karye. Kwace dai yana kallonsu, bai ce kome ba.

Mutumin nan ya ce da Idon Matambayi, "Duk irin makamin da ka ke da shi yau ka nuna mini !"

Da Idon Matambayi ya ji haka sai haushi ya kama shi ya tuna yana da ƙarfi. Ya rarumi mutumin da kokawa. Kokawa ta harƙe, ai nan kamar za a kada mutumin ya dire, shi kuma ya yi kamar ya kada Idon Matambayi ya dire. Daga can mutumin ya sami sa'a ya ɗauke shi sama, ya ƙwala shi da ƙasa ya taushe. Yana kansa sai Kwace ya zo ya kwaɗe shi da mari, ya gigice har ya rasa inda kansa ya ke. Ya sake kafe shi da tafi a ido, ya daɗa ruɗewa, har Idon Matambayi ya sami kansa. Suka

ɗebe ƙayansa, suka ce, "Je ka, mun bar ka, ba za mu kashe ka ba sabo da taurin kanka. Amma wata rana in an ce ka tari ɓarawo ba ka ƙara taryarsa ba." Sai ya yi tafiyarsa ya bar su nan tsaye.

An Yi Fashi, Ba Wurin Sa Kaya

SA'AN nan Kwace ya ce, "Babu abin da ya dame ni yanzu sai rashin wurin da za mu sa kayan nan a gidammu. Daɗin daɗawa kuma ga shi kayan ya yi mana yawa har ba za mu iya ɗaukarsa ba. Ina yadda za mu yi yanzu?"

Idon Matambayi ya kada baki ya ce, "Ai wannan ba wani abu ba ne mai wuya. Shin ba mu duba wani wuri a nan mai duhuwa liflif, mu ɓoye kayan har lokacin da muka sami dama mu ɗauke shi? A hankali a hankali da kaɗan kaɗan sai mu jide shi kaf."

Kwace ya ce, "I, haka za mu yi."

Da suka haɗa shawara a kan haka sai suka yi ta yawo cikin dajin nan, suna ta neman wuri mai duhuwa inda za su ɓoye kayan. Suka yi ta nema har Allah ya sa suka sami wuri. Daga nan fa suka komo suka yi ta jidar kayan, har suka jide shi kaf. Duk lokacin nan ba su san abin da ya ke cikin kayan ba, su dai sun ga kaya a ɗaure. Sai suka shiga kwance-kwance. Wani in sun kwance ba abin da za su tarar sai riguna bullan aska biyu biyu, wani kuwa ba kome sai tarkacen koli. Suna ta kwancewa dai har suka kwance wanda suka iske tsabar kuɗi a cikinsa fam ashirin da sule biyar da sisi. Da ganin kuɗin nan Kwace ya ce, "A ! Mu kam tsiya a wurimmu ta ƙare. Yanzu abin da za mu yi sai mu tafi gida da kuɗin nan, sauran kaya kuwa mu bar shi nan, har Allah ya kai mu gobe mu komo mu fara ɗauka, da ni da kai da Ɗauke."

Idon Matambayi ya ce, "I, sosai. Kuma wa ya san abin da Allah zai ba mu gobe ? Watakila mu sami fiye da wannan."

Kwace ya ce, "To, wannan dai sanin gaibu sai Allah."

Suka ɗauki kuɗin nan suka tafi da su gida gabannin magariba. Da isarsu gida sai suka iske shi ƙulle. Idon Matambayi ya tambaya da mamaki, "A'a ! 'Dauke bai dawo ba har yanzu, lafiya dai ?"

Kwace ya ce, "Kai, ba kome, an jima ka gan shi. Amma tun da mu ke tare bai taɓa yin dare irin na yau ba."

Suka buɗe ƙofa suka shiga, suka zauna suna jiran 'Dauke ƙatoƙato, ba su gan shi ba har kusan tsakar dare. Idon Matambayi ya sake cewa, "Yau me ya sami 'Dauke, ko an kama shi ne ?"

Kwace ya ce, "Haba, Idon Matambayi, daga mutum ya je sayen wani abu a gari sai a kama shi! In ka tona yanzu haka ma wani ya gani da 'yan kuɗinsa ya ke so ya raba shi da su. Kai dai har yanzu ba ka san 'Dauke ba." Idon Matambayi da jin zancen karɓar abin wani sai jikinsa ya yi ƙarfi.

Suka gaji da jira suka kwankwanta su ɗan gyangyaɗa. Barci ya fara ɗaukarsu sai 'Dauke ya iso ya shiga ɗakin, suna kwana. Da shigarsa sai Idon Matambayi ya yi firgigi, ya farka da magagin barci ya ce, "Kai wane ne ?"

"Ni ne."

"Kai wa ?"

"Ni ne dai."

Suna cikin haka karaf sai Kwace ya ji abin da su ke cewa, ya ce, "Haba, Idon Matambayi, don Allah ka buga masa irin ƙullin nan naka mana! Kana ganin mutum ya zo zai cuce mu!"

Da 'Dauke ya ga dai im bai faɗa musu ko wane ne shi ba za su kashe shi sai ya ce, "Ai ni ne 'Dauke."

Suka ce, "Dauke, barka da zuwa! Yau ina ka yi dare haka ?"

Dauke ya ce, "Mm, bari, ai yau Allah ya so ni, da kwaɗayina ya kai ni ga tsala!"

'Yanuwansa suka yi maza suka ce, "In ce ko dai ka samo mana ɗan abinci ?"

"I, na samo amma ba yawa, tsire na sayo."

Suka zauna suka ci ɗan tsiren nan da sauran abincinsu na gida, suka ƙoshi. Kafin su gama cin abinci asuba ta yi. Idon Matambayi da Kwace duk suna alla-alla Dauke ya ba su labarin abin da ya same shi. Suka ce, "To, Dauke yaya aka yi har ka yi dare haka ?"

Dauke ya ce, "Ku bari, ai tun da na zo duniya ban taɓa shan wuya, wuyar banza, irin ta jiya ba. Bayan kun fita kaɗan ni kuma na fita har na isa Kafi. Da shigata na yi ta yawo cikin Kafi kwararo kwararo, ko Allah ya sa na ga gidan attajiri wanda za mu kai wa hari. Na yi ta yawo na yi ta yawo tun hantsi har azahar. har la'asar, Allah bai nuna mini gidan ba sai ɗaya tak. Na duba shi ko ina ban ga ta hanyar da za mu ɓullo masa ba don sata. Katangarsa mai tsawo ce ƙwarai da gaske, samanta kama an kakkafa itacen gauɗe don kada a haura ta. Na duba na ga ƙyauren ƙofar gidan na ƙarfe ne. Ban da wannan ga shi cike da ƙatta tiƙatiƙa madaka kuka. Mai gidan kuwa a yadda na ji ba mai sarauta ba ne, attajiri ne, sunansa Musa.

"Da wani mutum ya zo zai wuce gabana lokacin da na ke ƙuƙulla zancen nan a zuciyata sai na ce da shi, 'Mai tafiya, don Allah in tambaye ka mana ba raini ba.'

"Ya ce, "Mene ne ?"

"Na ce, 'Don Allah, gidan sarkin garin nan ne wannan ?'

"Ya ce. 'A'a. gidan wani ɗan kasuwa ne mai kuɗi da yawa.'

"'Haka ne. To, shi kuwa mene ne cinikinsa ?'

"Ya ce, 'Goro a ke yiwo masa a yamma. Ban da wannan kuma yana sayen fata da gyaɗa in lokacinta ya zo, ya sayar wa Turawan Kamfani. Kai, har shanu ya kan saya a kai masa Ikko a sayar. '"

"Na ce, 'Shi kuwa haifaffen garin nan ne ?'

"Ya ce da ni, 'A'a, ba na yi maka ƙarya ba, ni ban sani ba, domin ni baƙo ne, bara na zo garin nan daga ci rani.'

"Na ce, 'Towo.'

"Na yi maza na ƙyale shi don kada ya farga da ni, na ce da shi, 'Shi ke nan.'

"Ya tambaye ni ya ce, 'To, kai kuwa me ya sa ka cika tambayar mai wannan gida ?'

"Na ce da shi, 'Ba kome, ca na ke gidan mai garin ne inda za ni in sauka.'

"'Zo mu je mana in nuna maka gidan mai garin."

"Na ce da shi don kada ya gane ni, 'A'a, na gode, kai dai nuna mini hanyar gidan.'

"Ya nuna mini, muka yi sallama. Daga nan ban ƙara ganinsa ba.

"Sai na ce, 'Allah na gode maka tun da na sami labarin gidan nan!"

Kwace da Idon Matambayi suka ce, "Sosai! Kwanan nan ma hare shi, mu ɗebe dukiyarsa kaf."

Dauke ya ci gaba da labarinsa, ya ce, "Kuna ji da kyau? Da muka rabu da mutumin nan rana ta kusa faɗuwa, na ce bari dai in tafi kasuwa ko na sami abin da zan saya wanda za mu ci yau. Da shigata kasuwa na kama hanya har wurin 'yan tsire, na je na sayi na sisi. Mai tsire ya zare ya ƙunshe mini a takarda. Na karɓa dai ke nan sai wani mutum ya wuce gabana, ga aljihun

kaftaninsa da ɗan tudu, na ga kuwa lalle tudun nan ba banza ba. Na yi ta binsa duk inda ya yi, har muka shiga cikin runtsin mutane. Na zo na gɛge shi kamar wanda zai wuce, na duƙa kaɗan na sa hannu cikin aljihun kaftanin, na sami jaka na ɗauke, ashe da kuɗi a ciki. Lokacin da na ɗauke kuɗin nan ashe wani mutum yana kallona, da ciro jakar sai ya buga mini kururuwa, "Barawo! Barawo!" Kasuwa ta yi caa a



kaina. Da na ga haka sai na tuna da guduna. Da dai na sami wani ɗam fili tsakanin mutane sai na sheƙa a guje, mutanen kasuwa kuma sai kallo da sallallami, na tsere kau da kuɗin nan a hannuna a riƙe kam."

Da jin haka sai Idon Matambayi ya tuna rana da ya yi sane irin wannan, sabo da haka ya yi murmushi ya

ce, "Ka ji ranarmu, ni ma haka na yi kwanakin baya, na tsere ba wanda ya kama ni."

Dauke ya ci gaba ya ce, "Na yi ta gudu na yi ta gudu, har na gaji na zauna na huta a bayan gari, na ajiye jakar a kusa da ni. Aka jima na tashi na soma tafiya har na kusa da gidammu, ban tuna ba kuwa na bar jakan nan a wurin da na huta. Da na ga ba jaka na yi maza na koma da gudu da gudu. Na isa na je ban ga jaka ba, na yi nema na yi nema, har na gaji na komo gida."

Da Dauke ya gama labarinsa 'yanuwansa suka ce, "Ai wannan ba kome ba ne, tun da Allah ya sa ka tsira, kuma ka samam mana gidan da za mu je mu kwashi dukiya idan Allah ya yarda. Ba kullum a ke kwana bisa gado ba."

"I, haka ne."

Ya Shiga Kogin Tunani

YAYIN da a ke zancen nan hankalin Idon Matamba-yi duk ya koma kan a yi wa Musa sata. Yana ta ƙuƙkulla shawarwari a zuciyarsa na yadda za su yi sata a gidan Musa.

Bayan da Dauke ya gama ba da labarinsa, ya ce, "To, ku yaya kuka yi? Kun sami ɗan abu dai jiya?"

Suka ce, "Haba bari, ai mu jiya addu'armu ta ci." Suka ba shi labarin duk abin da suka yi, da fashin kayan da suka yi, suka kuma nuna masa kuɗin da suka ɗebo daga cikin dukiyarsu ta fashi.

Da Dauke ya gani ya yi murna mai yawa. Amma da suka ba shi labarin sun bar kayan nan a wani wuri ransa ya ɓaci sosu, domin yana tsoron kada wani abu ya zo ya kwashe kayan nan, sabo da haka ya tambaye

su, ya ce, "To, ku kuwa me ya sa kuka bar kayan a wani wuri, kuma a ina ne ?"

Kwace ya ce, "Ka sani dai gidammu ba zai ɗauke dukiyan nan ba, sabo da haka ne muka nemi wani wuri inda ba wanda zai gane, muka ɓoye ta."

Da 'Dauke ya ji sun ɓoye kayan a wuri mai kyau, sai ransa ya kwanta.

Suna cikin zance har wani lokaci, sai Idon Matambayi ya ce da su, "A'a! Yau haka za mu wuni ne babu wata 'yar sata ?"

Suka ce, "Mu bari yau mu huta sai gobe in Allah ya kai mu, mu more, mu ci abinci ya kwanta mana sosai, mu sami damar barci, har ma mu warwasa wuƙaƙemmu da takubbammu, mu ƙara wa kibiyoyimmu dafi."

Ran nan tun daga fitowar rana har faɗuwarta ba abin da suka yi sai washin makamansu. Da la'asar suka tafi yawo, suka harbo barewa suka zo suka ƙyafe ta, ta ƙyafu, suka sa mata gishiri suka ci suka ƙoshi, suka koma suka kwanta. Gari na wayewa suka tashi daga barci, suka wanke fuskarsu suka sa rigunansu da wandunansu na ado.

'Dauke ya ce, "Shin ina ne kuka yi fashin nan, Kwace ?"

Kwace ya ce, "Wata 'yar duhuwa na nan kusa da inda muka saba yin fashi da kai, ka tuna ta ?"

'Dauke ya ce, "I , na tuna. Ko ba mai ƙaya-ƙayan nan ba ? Amma fa tana da 'yar tazara daga wurin da mu kan yi fashin."

Kwace ya ce, "Nan kuwa."

'Dauke ya ce, "Ina so yanzu ku tashi mu tafi in ga kayan nan don mu san yadda za mu yi da shi. Ni kam ban ga amfanin barinsa a dawa ba."

Idon Matambayi ma ya ce, "Ko ni ma ban gani ba. Yaya za mu sha wuya haka mu sami dukiya, mu zo mu

bar ta a daji ? To, in wani wanda ya fi mu so ya zo ya ɗauke ta fa, mu ce yaya ?"

Ko da ya ke Kwace ya farga cewa 'yanuwansa sun fi son dukiyan nan ta zo kusa da su, duk da haka ya ce, "Kai ka sani, Idon Matambayi, babu wurin da za mu sa dukiyan nan a gidammu. Abin da ya sa 'Dauke ya ke wannan magana, ai don bai ga yawan kayan ba ne."

'Dauke ya ce, "Ahaf ! Kome yawanta gara mu yi dabarar da za mu sa ta kusa da mu, da mu bar ta a can. Ko kuwa me kuka gani ?"

Idon Matambayi ya ce, "Yanzu abin da za mu yi sai mu gina rami mai zurfi a can,"—ya nuna wani wuri a cikin gidansu—"Mu shafe shi, mu daɓe ƙarƙashinsa, mu zuba kayan."

Kwace ya kada baki ya ce, "To, wani abu ba zai cinye dukiyar ba kamar gara ko ƙwari ?"

'Dauke ya ce, "Kwace da musu ka ke ! Shin ko sun ɓata mene ne ? Bai fi kyau ba da kayan su ɓaci a wani wuri nesa da mu ?"

Idon Matambayi ya ce, "Sosai, wannan hakanan ne."

Da Kwace ya gani duk 'yanuwansa sun haɗu kan shawara guda, sai shi ma ya yarda da su, amma ba da sonsa ba sosai. Idon Matambayi ya ce da su su ɗauki magirbi da dundurusu na haƙa. Suka ɗauka suka yi ta haƙa, sai da suka kwana uku cur suka gama. Da gamawarsu suka shafe shi ƙalau suka daɓe, kamar yadda Idon Matambayi ya shawarta.

Kashegari suka kama hanya, suka tafi wurin kaya. Da isarsu sai suka iske babu sauran kaya sai guda ɗaya tak ! Suka duba, suka ga sawun mutane da na jakuna cakacaka a wurin. Idon Matambayi ya yi mamaki mai yawa yana cewa, "A ! A ! Yau ga abin mamaki, ashe akwai wani irin mutum a duniyan nan wanda ya san ajiyarmu har da zai zo ya ɗiba !"

Ɗauke ya ce, "Ai ita na ke gaya muku, Kwace kuwa ya tsaya da musu ! Yau a duniyan nan kome ka ke taƙama, wani ya fi ka, in sarauta, in wayo, in ashararanci !"

Suka tsaya wurin nan suka daɗe suna mamaki, Kwace kuwa bai ce kome ba. Fushi ya kama shi da kunya, sabo da haka ya ce, "Yanzu abin da za a yi sai ku ku ɗauki ɗan kayan nan ku tafi gida, ni kuwa zam bi wannan sawu sai na ga inda ya je."

Saura suka yi shiru kaɗan, sa'an nan Idon Matambayi ya ce, "Ba na ce i ba, don ba mu sani ba ko waɗanda suka ɗebe kayan nan masu abinsu ne, ko kuwa waɗansu ne. Abin da na tabbata shi ne lalle mutanen da suka ɗauki kayan nan suna da yawa. Kada ka je su ji ma ciwo, ko a kama ka. Ko ba haka ba ne, Ɗauke?"

Ɗauke ya ce, "I, kai ma kana da gaskiya, domin kun faɗa mini cewa masu kayan nan suna da yawa. Kuma ran nan da ba don ku biyu ba ne lalle da mutumin nan ya kashe ka. Kada ka tafi, Kwace, mu zo yi biyu biyu, kamun gafiyar Ɓaidu. A gamu wata rana, mu haƙura."

Kwace ya ce, "To, shi ke nan."

Da kaiwarsu gida suka kwance ɗan kayan nan suka ga ba kome ciki sai rigunan Nufe manya-manya, suka yi ta murna, tun ba Ɗauke ba, shi da bai ga yawan kayan ba da. Suka ci abinci, suka huta.

Haramar Kai Wa Musa Hari

DA gari ya waye Kwace ya ce, "To, yau sai mu yi haramar kai wa Musa hari. Ina yadda za mu ɓullo masa ?"

Ɗauke ya ce, "Abin da ya dame ni ɗaya ne, kada in je nuna muku gidansa a kama ni sabo da sanen da na yi a kasuwa kwanan baya. Ina dabara ?"

Idon Matambayi ya ce, "Assha, wannan kuma abu ne mai wuya? Ga yadda za mu yi, mu sa tufafi masu kyau mu tafi garin kamar waɗanda suka zo cin kasuwa, kai 'Dauke kana gaba muna biye. Ka naɗa rawani ka rufe fuskarka, sai idonka kawai za a gani. Makamammu kuwa wani cikimmu ne zai ɗauke su a ƙunshe, ya zauna a bayan gari. In 'Dauke ya wuce gaba ya riƙa taƙama yana jefa ƙafa ɗai ɗai don mutanen Kafi su yi tsammani shi wani mai sarauta ne."

Dukan abin nan da Idon Matambayi ya faɗa suka yarda da shi, suka zaɓi wuƙaƙe mafiya kaifi guda uku da 'yar adda ƙarama. 'Dauke ya ɗauki rawani baƙi ɗankura, ciki goma sha biyu, kamu goma sha biyu, ya naɗa ya rufe fuskarsa rif, sai idanunsa a ke gani kaɗan. Kuma sauran 'yanuwansa suka ɗauki 'yar ciki ɗai ɗai da riga guda guda suka sa, suka kama hanya suka tafi.

Suna cikin tafiya sai 'Dauke ya ce, "Allah ya ɗora mu bisa kan wannan mutum!"

Saura suka ce, "Amin! Amin!"

Suka yi ta tafiya har suka isa Kafi. 'Dauke ya nuna wuri a wajen gari ya ce, "Mu tsaya nan mu bar kayammu, ɗaya ya zauna jirammu, ɗaya kuwa ya biyo ni mu tafi. Wa zai bi ni? Wa zai zauna jira?"

Idon Matambayi ya ce, "Mu tafi tare, Kwace kuwa ya zauna har mu dawo, shi kuma ya tafi da kai, ni in zauna."

Kwace ya ce, "To." Ya tattara wuƙaƙensa ya sa mayani ya rufe ya ɗaure, ya hau kansu ya zauna, don kada wani mutum ya zo ya gane abin da ya ke ciki, da shi da 'yanuwansa.

'Dauke ya ce, "Taso mu je, Idon Matambayi, kai Kwace sai mun dawo."

"Allah ya dawo da ku lafiya."

"Amin?"

Suka shiga cikin Kafi, Ɗauke yana gaba Idon Matambayi yana biye, su kurɗa nan su kurɗa can har suka hango gidan Musa. Ɗauke ya ce wa Idon Matambayi, "Ka ga wani dogon gida haka mai shafen laso a sorayensa?"

"I, na gani."

"To, gidan ke nan."



Suka yi ta tafiya har suka zo kusa da ƙofar gidan Musa suka tsaya, Ɗauke ya ce wa Idon Matambayi, "Ina yadda ka ga za mu yi wa gidan nan? Ga shi ba ya hawuwa sabo da tsawon katangarsa da gauɗen da ke bisanta, ga kuwa makullin ƙofar gidan na ƙarfe ne."

Idon Matambayi ya ce, "Mu daɗa zagawa dai har mu ga bayan gidan."

Da suka zaga shi sai suka ga gidan duk yana kewaye da gidajen makwabta. Alhasali dai suka rasa ta hanyar da za su ɓullo wa gidan nan su yi sata.

Idon Matambayi ya ce, "Babu shakka sata gidan nan lalle yadda ka ce ne sai an shirya. A yanzu ban ga yadda za mu yi ba, sai dai mu koma wurin Kwace, mu ba shi labarin gidan duka, shi kuma in zo da shi ya gani, kai kuwa ka zauna maimakonsa."

'Dauke bai yi musu ba, ya ce, "To, haka za mu yi."

Suka kama hanya suka tafi wurin Kwace da la'asar lis. Da isarsu, Kwace ya yi farad da baka ya ce, "Yaya mu tafi ne yanzu gidan Musa, ko sai dare ya yi."

'Dauke ya yi masa gatse ya ce, "Haba Kwace, ai ko Mayyar Soba wacce ta yi sata lahira ba ta yi sata yanzu ba !"

Kwace da jin gatsen nan ransa ya ɓaci ya yi fushi mai yawa. Sabo da fushin nan ba zai amfane su ba. Idon Matambayi ya ce, "Yanzu a cikimmu bai kamata ba mu rika fushi da juna ba, kun sani fa Allah ne ya sada mu."

Da jin wannan magana sai ran Kwace ya yi fari, ya huce. Idon Matambayi ya ba shi labarin gidan duka yadda ya ke.

Kwace ya ce, "Ashe haka gidan ya ke ?"

Idon Matambayi ya ce, "Sosai, ko shakka kada ka yi. Yanzu kai 'Dauke sai ka zauna nan, mu tafi da Kwace ya je ya gano gidan nan, ko ma san wace mu ke ciki."

'Dauke ya ce, "Da almuru haka ? Kun tuna fa gidammu da 'yar tazara daga wurin nan."

Idon Matambayi ya ce, "Yanzu abin da ya fiye mana mu bar wannan abu sai gobe, kai 'Dauke tafi kasuwa ka sayo mana dan abin da ma ci yau."

Sun Gamu Da Batsokana

SAI 'Dauke ya tafi kasuwa ya je ya sayo cinyar rago mai mai, da gwangwanin sigari guda, da goro guda hudu kursakursa, da nakiya cike da zuma, ya komo wurin 'yanuwansa. Suka kama hanya suka tafi cikin dare, suna ta tafiya suna zance har suka kusa da gidansu. Bayan sun haye wani dan kwazazzabo sai suka gamu da wani mutum yana tafiya shi kadai tal, babu kome a wurinsa sai wata kokara katuwa a kafadarsa a sabe. Da mutum ya gan shi ya ga barawo kuntukurmi. Da suka gamu da mutumin nan ya wuce bai ce da su ci kanku ba, suka wuce. Ba su dade da gamuwa ba sai Idon Matambayi ya ce da 'yanuwansa, "Kai, wannan abu raini ne ! Yaya kamarmu mutum zai gamu da mu a daji irin wannan da tsakar dare haka kuma, ko ya ce da mu 'Sannunku !' "

'Dauke ya kada baki ya ce, "Watakila tsoro ne ya yi masa yawa har ya kasa magana da mu."

Kwace ya ce, "Tsoron me ? Ba tsoron kome sai girman kai. Na san halin irin 'yam fashin nan, domin fashi aikina ne tun da dadewa, ko da rana ko da dare. Yanzu haka ba wani abu ba ya sa ya ki yin magana da mu sai don ya burge mu, mu ce wai shi wani jaruni ne. Yana zaton mu kananan 'yam fashi ne. In ka tona da kyar ne shi ma ba barawo ba ne !"

Idon Matambayi ya ce, "In kuwa haka ya ke tsammani, bari im bi shi ya ga iyakarsa yau, ku kuwa ku biyo ni a hankali, domin ni na fi ku gudu."

'Sai ya kwashe a guje sai ka ce barawon asuba. Kafin a jima ya iske mutumin nan yana tafiya. Ya ce, "Kai mai tafiya, kai mai tafiya, tsaya nan !"

Mutumin ya tsaya har Idon Matambayi ya iso ya ce, "Ina ka fito, ina za ka cikin wannan dare ?"

Mutumin ya ce, "Me ye ruwanka da inda na fito, balle inda za ni ? Ka aike ni ne ? Ko kuwa na fito don ƙananan 'yam fashi irinku ne ? Na ga tun da muka gamu ranka ya yi shawarar ka tare ni."

Yayin da Idon Matambayi ya ji wannan magana ya yi murmushi, ya ƙyalƙyale da dariya, yana ganin wautarsa. Kafin su ƙulla wani abu Kwace da'Dauke sun iso.

Kwace ya tambayi Idon Matambayi dalilin dariyarsa da murmushinsa lokacin da suka iske su. Idon Matambayi ya amsa wa Kwace ya ce, "Bari Kwace, ai yau mun gamu da mai izgili !"



Mutumin ya ce da Idon Matambayi, "A ! Ba Kwace ba, don Allah ka ce 'Fizge' ma, duk ku ukun nan kun yi kaɗan, amma ni yanzu ba zan yi muku kome ba sabo da kai, Idon Matambayi.

Dauke ya kada baki ya ce, "Ahaf ! Yo mu kuma za a ci da buguzun ? Mun gaji da gafara sa sai mun ga ƙaho ! Kai dai in kana so mu ƙyale ka da lalama mu ƙyale ka, amma kada ka kawo mana burga nan !"

Mutumin nan da jin zancen Dauke, sai zuciyarsa ta ɓaci, ya ce, "To, yanzu duk abin da ku ke da shi na wajen mugunta ku yi mini in gani."

Da jin haka sai Kwace ya zaro wuƙa zai daɓa wa mutumin, sai hannunsa ya sage. Dauke kuma ya rugo da gudu ya kama shi da kokawa, sai jikin mutumin ya riƙa bin Dauke kamar wanda ya ke jan alewa. Idon Matambayi ya kai masa irin ƙullin nan nasa a ciki sai hannunsa ya ɗafe. A'a! Mutumin nan dai yana kallon ƙoƙarin kowa a banza. Ya tambaye su ya ce, "In ce ko yanzu kun san ku ba kowan kowa ba ne ?"

"I, mun sani, kowa da wanda ya fi shi."

Ya ce da su, "Ba don Allah ya sa da kyakkyawan yaron nan ku ke ba, yau da kun ga iyakarku, da kuwa kun san ba burga a ke muku ba !"

Suka ce, "Mun gode, mun gode, Allah kuwa ya bar dalili ya ƙara soyayya a tsakaninku."

Idon Matambayi ya ce, "Baba, mun tuba, ka yafe mu."

"A'a! Ba kome ɗan nan."

Shi ke nan, Kwace ya sami kansa, hannunsa ya sauka ƙasa, Idon Matambayi kuma ya sami kansa ya rabu da mutumin.

Mutumin ya ce, "Kun gani da ma abin da ya sa na yarda hannun yaron nan ya liƙe a jikina don kada in ƙyale sni ku yi tsammani ko yana da wata karama ce."

Idon Matambayi ya tambayi mutumin nan sunansa, ya faɗa masa ya ce sunansa Batsokana. Bayan nan kuma ya ce, "To, Batsokana, yanzu ina za ka cikin wannan dare ?"

Da suka zaga shi sai suka ga gidan duk yana kewaye da gidajen maƙwabta. Alhasali dai suka rasa ta hanyar da za su ɓullo wa gidan nan su yi sata.

Idon Matambayi ya ce, "Babu shakka sata gidan nan lalle yadda ka ce ne sai an shirya. A yanzu ban ga yadda za mu yi ba, sai dai mu koma wurin Kwace, mu ba shi labarin gidan duka, shi kuma in zo da shi ya gani, kai kuwa ka zauna maimakonsa."

'Dauke bai yi musu ba, ya ce, "To, haka za mu yi."

Suka kama hanya suka tafi wurin Kwace da la'asar lis. Da isarsu, Kwace ya yi farad da baka ya ce, "Yaya mu tafi ne yanzu gidan Musa, ko sai dare ya yi."

'Dauke ya yi masa gatse ya ce, "Haba Kwace, ai ko Mayyar Soba wacce ta yi sata lahira ba ta yi sata yanzu ba !"

Kwace da jin gatsen nan ransa ya ɓaci ya yi fushi mai yawa. Sabo da fushin nan ba zai amfane su ba. Idon Matambayi ya ce, "Yanzu a cikimmu bai kamata ba mu riƙa fushi da juna ba, kun sani fa Allah ne ya sada mu."

Da jin wannan magana sai ran Kwace ya yi fari, ya huce. Idon Matambayi ya ba shi labarin gidan duka yadda ya ke.

Kwace ya ce, "Ashe haka gidan ya ke ?"

Idon Matambayi ya ce, "Sosai, ko shakka kada ka yi. Yanzu kai 'Dauke sai ka zauna nan, mu tafi da Kwace ya je ya gano gidan nan, ko ma san wace mu ke ciki."

'Dauke ya ce, "Da almuru haka ? Kun tuna fa gidammu da 'yar tazara daga wurin nan."

Idon Matambayi ya ce, "Yanzu abin da ya fiye mana mu bar wannan abu sai gobe, kai 'Dauke tafi kasuwa ka sayo mana ɗan abin da ma ci yau."

Idon Matambayi ya ce, "Wace irin wuya ce wannan?"

Batsokana ya ce, "Abin da na ke so im faɗa shi ne yin sata gidan Musa ba kullum ta ke da wuya ba, haka kuma fitar da kayan satar. Wuya ɗaya na nan ita ce tsananin gadi a garin. Ga shi kuwa sarkin gadi yana da wayo da hila mai yawa, ɓarawo yanzu im bai yi hankali ba a Kafi ya zo hannu."

Idon Matambayi ya ce, "To, mu dai muna ga Allah muna gare ka, ka taimake mu mu san yadda za mu washe Musa."

Batsokana ya kada baki ya ce, "To, na ji. Yanzu abin da na ga za mu yi sai ko wannenku ya je Kafi ya yi sata sau ɗaya, mu ga yadda zai yi ya kuɓuta daga Sarkin Gadi Sani, kuma ma san dabarar da za mu yi."

'Dauke da Kwace suna jin duk abin da Batsokana da Idon Matambayi su ke ƙullawa, ba su ce kome ba. Daga nan 'Dauke ya ce, "Gaskiya ne da a ke cewa inda kwaɗayi da wulakanci, kowa ya sa zuciyarsa a kan abin wani dole ya jure wa wahala. 'Dauri a wurimmu, da rauni, da dukan kawo wuƙa, muna tare da su. Duniya kuwa haka ta gada, wata rana samu, wata rana kuwa rashi ko ɗauri."

Kwace ya ce, "Allah ya sa mu a wajen samun dai kullum, mu kashe Sanin mana mu huta da shi."

Idon Matambayi ya ce, "Im mun kashe shi sai a naɗa wani wanda ma wataƙila zai fi shi wayo."

Kwace ya ce, "Kai! Magaji magaji ne."

"An sani, amma ba haka ba ne kullum."

Batsokana ya ce, "Wa zai fara zuwa Kafi sata?"

Kwace ya ce, "Ni ne."

Wayon Sata Irin Na Kwace

DA yin almuru Kwace ya yi haramar tafiya sata a Kafi, ya fito gida. Da zai fito ya ɗauki kwari da baka, da takobi babarbare, da wuƙaƙe guda biyu manya manya. Da shigarsa Kafi sai aka busa ƙahon shaidar fara doka. A lokacin nan kuwa kowa aka gani a waje ko da ɗan sarkin garin ne sai a kama shi, sabo da tsananin doka. Ya kama hanya yana tafiya cikin lokoki, bai aune ba sai yana kan titi. Ya bi titin kaɗan sai can ya hango wani mutum yana tafe baƙi ƙirin, ashe ɗan gadi ne. Allah ya sa ɗan gadin bai gan shi ba, sai ya duba dama da shi sai ya ga wata 'yar hanya, ya bi ta ya bar titin, don kada ya gamu da ɗan gadin da ya hango. Ashe hanyar da ya bi cikin gida ta shiga, yana cikin binta sai ya yi aune yana cikin gida tsundum! Ga mutum biyu suna zaune a kan daɓen ƙofar wani ɗaki suna hira. Kwace ya rasa yadda zai yi, sai wata dabara ta zo masa. Ya rufe idanunsa kamar makaho, ya ce da su, "Allah zi wahidun, bayin Allah, ko kun ci kun rage ku bai wa makaho!" Lokacin da ya ke faɗar maganan nan duk ya sake murya tasa ta zama kamar ta almajiri.

Wani a cikin masu hiran nan ya ce, "Bara yanzu da dare?"

Dayan ya ce, "Kai, ɓarawo ne! Amma bari mu je mu gan shi."

Da isarsu wurin Kwace sai suka iske makaho ne, idanunsa a rufe rif. Suka ce masa, "Kai ko baƙo ne a garin nan? Wa ya ke bara bayan an yi busa?"

Kwace yana marairaita, ya ce, "Wallahi, ban sani ba, yau na zo garin nan, ga sni yunwa tana neman ta kashe ni."

Da suka ji haka sai tausayinsa ya kama su, suka kawo masa abinci ya ci, suka ba shi tabarma da ɗaki ya kwana har gari ya waye. Da jin haka Kwace ya yi murna gaya matuƙa, ya yi ta musu godiya irin ta almajirai. Ya riƙa cewa, "Allah ya ji ƙan mahaifa, ya gama su da gafara, Allah ya fisshe ku sharrin maƙiya !"

Da ya gama ya tafi ya kwanta, masu gida su kuma suka tafi ɗakunansu suka kwankwanta. Da yin asuba sai Kwace ya tashi ya tafi wani ɗaki a gidan ya isa ya iske ƙofarsa tana rufe da ƙyaure, ya tura ƙyauren a hankali ya ji shi dandan. Ya daɗa tura shi da ƙarfi sai ƙyauren ya buɗe ya saka ƙafarsa ta dama a cikin ɗakin, ya jima kaɗan bai ji motsi ba, ya sake saka ƙafar hagun ya tsaya kaɗan bai ji motsi ba. Mai ɗaki yana ta sharar barci. Daga nan ya ɗauki ashana ya ƙyarta, ya ga cikin ɗakin duk. Ya yi ta sanɗo ya yi ta sanɗo har ya kai wurin wani akwatin ƙarfe, ya ɗaga shi ya ji shi da nauyi, ya kuma sake jinjina shi. Yana cikin niyyar ya ɗauke shi sai mai ɗakin ya farka, ya yi salati irin wanda a ke yi in am farka daga barci. Da Kwace ya ji mutumin nan ya farka, sai ya yi maza ya fito a guje. Mai ɗaki ya kwarma ihu, duk gida aka fito. Kafin su fito kuwa Kwace ya yi nisa da gudu. Don kada 'yan gadi su kama shi a hanya ya yi maza ya shiga ƙarƙashin kadarko a kan titi. Da 'yan gadi suka ji ihun ɓarawo suka yi maza suka tafi gudummuwa. Suka zage unguwan nan kaf har suka riƙa wucewa kan kadarkon da Kwace ya ke ƙarƙashi, suna cewa, "Yau Allah ya so wannan mutum!" Kwace yana jinsu. Suka gaji da nema, suka tafi.

Da asalatu ta yi, Kwace ya zaro jiki ya fito, ya kama hanya ya yi tafiyarsa. Kafin ya isa Sauke-mu-raba gari ya waye. Da isarsa ya tarar 'yanuwansa suna zazzaune suna zance. Suka tambaye shi yadda ya yi a Kafi. Ya

ɗaɗa musu duk abin da ya same shi. Aka jima kaɗan ya ɗauki abinci ya ci, ya koma ya zauna tare da 'yanuwansa.

Batsokana ya ce, "To, kun ga irin dabarar da Kwace ya yi tana da kyau, kuma ina so kowa a cikinku ya yi irinta. Idan kuka yi haka ba na shakka zan iya fitad da dabarar sace kayan Musa duka. Duk karkaran nan ba mai dukiyar Musa. Idan Allah ya ɗora mu a kansa muka washe shi, dukammu mun sami dukiyar ɓatarwa har wani lokaci mai tsawo, watakila ma daga nan kome ya ishe mu, mu bar sata."

Yayin da Batsokana ya gama wannan magana sai zuciyarsu ta daɗa ƙarfi, tun ba ta Idon Matambayi ba. Sabo da haka ya ce, "Shin ban da Sani akwai wani wanda zai dame mu ya hana mu sakewa ?"

Batsokana ya ce, "A! Na tabbata yanzu ana nan ana ta diddigin ɓarawo a Kafi. Na san halin mutanen Kafi, domin idan ɓarawo guda ya shiga gida ɗaya, a kan yi wata biyar ana nemansa."

'Dauke ya dubi 'yanuwansa, ya ce, "Ni za ni Kafi yau in Allah ya yarda. Da ikon Allah kuwa lafiya zan komo, im ma na ga da hanya sai in zo da 'yan kuɗi."

Saura suka ce, "Allah ya nufa!"

'Dauke ya ce, "Sai dare ya yi tukun zan tafi."

"To, Allah ya kai mu."

Wayon Sata Irin Na 'Dauke

DA yin dare sai 'Dauke ya yi shirin tafiya Kafi, ya ɗauki kayan sata duka da makami ya tafi. Da zai tafi ya ce da 'yanuwansa, "To, ni kam zan tafi, in kun ga shiru har gobe wajen hantsi ban komo ba, ku ɗebe shakka, an kama ni."

Suka amsa suka ce, "To, Allah ya komo da kai lafiya, mu ba mu fatar a kama. Da yardar Allah gida za ka komo ƙalau."

'Dauke ya kama hanya ya tafi. Yana tafiya bai gamu da ko kare ba a kan hanya har ya isa Kafi, ya shiga garin ya yi ta tafiya. Ya shiga nan ya faɗa can, har ya sami wata 'yar hanya ya bi. Bai daɗe yana binta ba, sai ya ji a hankali ana cewa, "Dana kibiyarka da kyau, da ya zo ka ɗora masa."

Da ya ji maganan nan sai jikinsa ya ɗau rawa farfar, tsoro duk ya kama shi. Ya yi maza ya sake hanyar da ya ke bi da, ya bi wani ɗan kurɗe. Bai daɗe ba kuma yana binsa sai ya ji kudu da shi ana cewa, "Mutumin can da ke tafe lalle ɓarawo ne, domin im ba ɓarawo ba, ba wanda zai fito yana yawo cikin garin nan da dare. Watakila ma ɓarawon jiya ne wanda ya ɓace mana a kadarko."

Da ya ji haka ya duba ko ina bai ga inda zai ɓoye ba. Ya daɗa ci gaba kaɗan sai ya ga wata 'yar kwana tsakanin katanga da katanga, ya je jikin 'yar kwanar ya yi lif, ko numfashi sai a hankali ya ke yi. Bai daɗe ba da tsayawa sai ga 'yan gadi biyu suna cewa, "Ba yanzu yanzun nan muka hango mutum ba, yaya ya ɓace mana da wuri haka ?"

'Dayansu ya ce, "Watakila ya bi rariyar can, ya ɓulle haka."

'Dayan ya ce, "To, mu bi can."

Suka tafi suka daɗe ba su dawo ba, 'Dauke yana tsaye, ko motsi bai yi ba. Sun jima da tafiya sai zuciyar 'Dauke ta yi masa shawara ya sake wuri, domin watakila im ba su same shi ba za su komo wurinsu na da, sai ya kama hanya ya yi tafiyarsa. Yana cikin tafiya sai ya riƙa jin gabansa yana faɗuwa ba gaira ba dalili. Ya ce a zuciyarsa, "Lalle faɗuwar gaban nan ba banza banza ba, bari in shiga masallacin nan im ɓuya har kusan asuba.

Da shigarsa masallacin sai ya ji tafiya tif tif a kan

hanya, ana cewa, 'Wallahi, a baya muka bar shi. watakila ma yana nan a jikin 'yar konar can."

"Ranka ya dade! Ranka ya dade! Sani Sarkin Gadi ya zo.

"Me ku ke yi nan ?"

"Yallabai, wani barawo mu ke bi tun dazun, ga shi ya bace mana."

"A ina ?"

"Daga haka muka yiwo kansa, sai muka iske ya tafi. Muka yi gaba muka yi baya, ba mu gan shi ba."

Sani ya ce, "To, barayi fa sun dame mu a garin nan, jiya na sami labarin wani ya shiga gidan Malam Isa. Watakila shi kuka gani yau. In kun tona lalle suna da yawa a wani wuri. In Allah ya yarda sai mun kare su duk! Ba ku duba inda sawunsa ya yi ba ?"

"A'a."

"Aikin banza ke nan. Daga yau ku rika lura da inda sawun mutum ya yi. Kun duba masallacin nan ?"

"Ranka ya dade, wane barawo ne don shegantaka zai shiga masallaci ?"

Daga nan suka rabu, kowa ya kama aikinsa.

Bayan sun dade da tafiya 'Dauke ya fito daga cikin masallaci, yana tafiya yana shawarar ko ya tafi gida ko kuwa ya shiga gidan wani ya yi sata. Haka ya yi ta yi, har ya kulla shawarar yin sata. Ya kama hanya ya yi ta tafiyə, in ya hangi 'yan gadi daga nesa ya yi maza ya sake turba. Ya yi ta yin haka cikin Kafi har ya yi niyyar shiga wani gida. Gidan nan kuwa kusa da ganuwa ya ke, sabo da haka da an koro shi sai ya yi maza ya haura garu ya tsere. Ya duba kofar ya gan ta a kulle. Ya zazzaga gidan don ya samu wurin haurawa, bai samu ba. Ya dada zagawa sai ya ga wani wuri da ruwan damina ya zage. A wurin zagewan nan ya sami 'yan matakalar da ya kama ya dira cikin gidan.

Da shigarsa ya nufi wani ɗakin hayi, ya je ya taɓa ƙyauren ƙofa ya ji shi a kulle dandan. Ya duba ƙyauren da kyau, bai ga ko 'yar kafar da zai saka hannunsa ba. Yana dubawa dai sai ya ga wata 'yar ƙusa daga gefen ƙyauren. Ya ja ƙusar, duk a banza.

Da ya ga dai ba yadda zai shiga ɗakin sai wata shawara ta zo masa ta kunna wa ɗakin wuta. Ya ga idan ɗakin ya kama wuta ya sami damar yin sata a wani ɗaki. Daga nan sai ya ɗauki ashana ya ƙyarta ya jefa a kan ɗakin, shi kuwa ya koma bayan wani ɗaki ya laɓe. Kafin a jima kaɗan, wuta ta kama, mai ɗaki ya yiwo waje da sauri, yana ihu, "Wuta ! Wuta ! Ihu ! Ihu !"

Da jin ihun nan mutanen gida da maƙwabta duk suka fito gudummawa. Waɗanda suna jin tsoron kada wuta ta kama ɗakunansu, suka yi ta fitad da kayansu a gigice. Da 'Dauke ya ga haka, sai ya fito ya riƙa kamar wanda ya zo gudummawar wutar. Yana zazzagawa sai ya ga wani ɗan kwatashi a ajiye, ya tafi ya jinjina sai ya ji shi da nauyi. Ya buɗe ya iske shi cike da kuɗi sule sule da fataka fataka, ya tara rigarsa ya juye kuɗin ya yi tafiyarsa. Yana cikin tafiya sai ya gamu da ɗan gadi a hanya.

"Kai, ina za ka ?"

"Gida za ni, na fito daga wurin gobara ne."

Da haka ya rabu da ɗan gadin nan, ya yi tafiyarsa. Da isarsa dutsen Sauke-mu-raba, sai 'yanuwansa suka yi ta murna sabo da abin da ya kawo. Suka wuni nishaɗi da shaye-shaye, da dararraku, kamar ko wannensu an naɗa masa sarautar wani babban gari. Amma tun da 'Dauke ya komo da kuɗin nan, Idon Matambayi ya dinga fargaba, ya riƙa cewa, "Allah ya fisshe mu kunyar 'yanuwa !"

Mutanen Kafi ba su kashe wutan nan da 'Dauke ya sa ba sai da ta ƙone gida biyar da kaya mai yawa. Bayan da wuta ta ƙare, kowa yana neman kayansa da ya tsira.

"Ina kika sa ɗan kwatashin kuɗimmu ne, Amina ?"

"Af ! Ai lokacin da wuta ta tashi, shi na soma ɗauka na fita da shi da magagin barci." "Ina kika sa shi ?" "A zatona dai wurin can na sa shi."

Da zuwansu wurin sai suka iske kwatashi ba kome. Suka dubi juna, suka yi salati da sallallami kamar waɗanda aka yi wa mutuwa. Suka yi ta cewa, "Allah Mai Girma ! Allah mai arzutawa, mai tsiyatawa ! Ba wani Sarki sai Allah. 'Yan kuɗin nan namu da mu ke maƙo-maƙo da su yau ga shi an ɗauke su sa'a ɗaya." Suka tafi gida suna mamaki da baƙin ciki.



Kashegari mutane suka yi ta zuwa suna jajen wuta da na sata. Da sarkin Kafi ya sami labarin wuta da sata sai ya sa aka kira mai gida da 'Dauke ya sa wa wuta. Da zuwansa ya durƙusa ya ce, "Ranka ya daɗe."

Fadawa suka ce, "A gaishe ka Lawal !"

Sarki ya ce, "Lawal, abin da ya sa na kira ka, ina so in san ainihin yadda ɗakinka ya kama wuta da dare jiya."

Ya ce, "Ranka ya daɗe, da dare can kusan asuba ina kwance ina barci sai na ji hayaƙi ya turnuƙe a cikin ɗaki. Da na farka na duba sai na ga wuta ta soma huda ɗakin. Na yi maza na yi ta ihu, mutanen gida da maƙwabta duk suka fito. Kafin mu kashe ta har ta ci gida biyar. Iyakacin abin da na sani ke nan."

Sarki ya ce, "Ba ka san wanda ya sa wutar ba ?"

Ya ce, "A'a."

"Shi ke nan, tafi gida."

Aka jima kaɗan sarki ya ce a tafi a kira masa Sani Sarkin Gadi. Da zuwansa ya faɗi ya yi gaisuwa. Sarki ya ce da shi, "Ka ji ka ji abin da aka yi jiya a gidan Lawal, ina dabara ?"

Sani ya ce, "Ranka ya daɗe, ba wanda ya sa wutan nan sai ɓarawo, dalilin kuwa da ya sa ya yi haka, don ya ga ba hanyar da zai yi sata a daren 'yan gadi ba su kama shi ba. Da daddare, mun ga wani ɓarawo, muna bin sawunsa sai na ji wuta ta tashi.' Kuma abin da na ke zato lalle ɓarawon nan ba ɗaya ba ne, suna da yawa a wani wuri. In an tona watakila wani mai samu su ke so su yi wa sata.

Sarkin Kafi ya ce, "To, na ji abin da ka ce. Ina yadda za mu yi mu rabu da su ?"

Sani ya ce, "Sai mu nemi wurin da su ke, mu je mu kame su duk. Shekaranjiya da muka kori wani ɓarawo kudu ya yi wajen hanyar Sauke-mu-raba. Watakila cikin dutsen su ke zaune."

Da ya gama zancensa ya fita ya tara 'yan gadi duka, ya ce musu, "Kun ga sata ta soma yawa a garin nan, ya kamata mu yi ƙoƙari mu hana ta. Idan kun kori ɓarawo ku dubi sawunsa da kyau da kuma hanyar da ya bi. Ta haka ma san yadda za mu ƙare su kaf."

'Yan gadi duk suka amsa maganar sarkinsu.

KAMAR yadda muka ce ɗazun ɓarayin Kafi sun wuni murnar kuɗin da Ɗauke ya sato. Batsokana ya ce musu, "Wallahi, waɗannan yara za ku zama kuntukurman ɓarayi, domin kowa a cikinku na ga yana da wayon fitad da kansa ko an kama shi. Ba na shakka za mu ɗebe dukiyar Musa kaf. Abin da ya dame ni har yanzu shi ne Sani Sarkin Gadi, domin yanzu yana nan yana ta neman hanyar da zai kama mu."

Idon Matambayi ya ce, "Yau watau ni ne da tafiya ko?"

"I, kai ne mana. Sai ka yi haramar tafiya da wuri."

Idon Matambayi ya ce, "Ai ni ba zan tafi ba sai na daidaici lokacin da aka fara gadi a garin."

Da dare ya soma yi Idon Matambayi ya ɗauki tufafin sata ya shiga, ya ɗauke wuƙaƙe uku da takobi ya saɓa, ya yi sallama da 'yanuwansa, ya fita.

Da shigarsa Kafi sai ya hangi ɗan gadi a tsaye. Ya yi maza ya sake hanya kafin ɗan gadi ya gan shi. Allah ya sa bai gan shi ba. Yana cikin tafiya sai ya yi kaciɓis da wani ɗan gadi a hanya. Ɗan gadi ya ce da Idon Matambayi, "Kai, ina za ka?"

Idon Matambayi ya ga ba shi da maraba, sai ya yi farat ya ce, "Sata."

"Sata?"

Idon Matambayi ya ce, "Ka yi shakka ke nan!"



'Dan gadi ya kai wa Idon Matambayi duka da sanda 'ya same shi. Idon Matambayi ya yi fushi, ya yi maza ya zare takobi ya fille kan ɗan gadi, ya faɗi matacce. Ba a jima ba sai wani ɗan gadi ya iso. Da ya iso ya ga ɗanuwansa a mace, kuma ga Idon Matambayi da takobi a hannu, sai ya yi nasa waje bai ce kome ba. Idon Matambayi yana ta tafiya ya duba wannan gida ya duba wannan, duk bai shiga ba. Yana kan haka a kan titin mota sai ya hango wani mutum a kan basukur yana tafiya. Da ganinsa sai ya ji gabansa ya yi ras, ya ce a ransa, "Mene ne zai same ni yau a cikin daren nan ?" Sai ya yi kwanciyarsa a tsakar titi kamar mai barci.

Da isar mai basukur wurin Idon Matambayi sai ya ce, "Kai, tashi ! Ya yi ta faɗar haka har sau biyar, sa'an nan Idon Matambayi ya tashi. Da tashinsa sai mai basukur ya ce, "Kai, me ya sa ka ke barci a kan turba da dare haka ?"

Idon Matambayi yana marairaita ya ce, "Ni, ni baƙo ne, baƙo ne, na shigo da dare ban san gidan kowa ba ko."

Mai basukur ya ce, "Ba ka san kowa ba, to, me ya kawo ka garin ?"

"Ai na sani."

"Wa ka sani ?"

"Idi."

"Idi na wace unguwa ?"

"Ban san unguwarsu ba."

"Shin Idin gajere ne, ko dogo ne ? Baƙi ne, ko fari ne? Siriri ne ko kakkaura ne ?"

Da Idon Matambayi ya ga mutumin yana neman ya ƙure shi, sai ya ce, "Kai duk ban sani ba, kada ka dame ni da yawan tambaya kamar Nasara !"

Mutumin ya ce, "Kai kuwa yanzu ina yadda ka ke so ?"

Idon Matambayi ya ce, "Ina yadda na ke so, ko ina yadda ka ke so ? Ko da a ke ce mini Idon Matambayi ai ba irin wannan tambaya a kan yi mini ba !"

Mai basukur ya ce, "Munafuki ! Barawo ! Ka zo ka yi mana sata, ka bar mu da jidali, yau Allah ya kam maka !"

Idon Matambayi ya ce, "Allah ya kam mini, ko ya kam maka ?"

Mai basukur ya ce, "Kai, ni ne fa Sani, sarkin gadin Kafi !"

Idon Matambayi ya ce, "Ba sarkin gadin Kafi ba, ko sarkin gadin lahira ne, yau Allah ya kam maka kai ma !"

Suna cikin haka sai Sani ya ɗauki usur ya busa. Nan da nan sai ga 'yan gadi bakwai. Suna shirin su kama Idon Matambayi, sai ya rika ja da baya kamar wanda zai gudu. Yana ta ja da baya suna binsa, har ya sami dama ya zaro wuka daga kube. Da ya rika ta a hannunsa sai sarkin gadi ya yi kusa da shi zai kama shi. Yana isa Idon Matambayi yana sukansa da wuka a kahon zuci. Sai Sani ya faɗi matacce. Sauran 'yan gadi kuma suka yi ta mutuwa, gama duk wanda ya yi niyyar kama Idon Matambayi a cikinsu, ran nan ya halaka. Sauran 'yan gadi da ba su mutu ba, suka yi ta bushe-bushe. Kafin a jima 'yan gadi goma suka zo. Da zuwansu suka ga sarkinsu da mutum uku a mace, Idon Matambayi kuwa a tsaye waje ɗaya da wuka a zare. Cikinsu ba wanda ya iya kama shi. Da ya ga mutane sun fara yin yawa ya sani sarkin yawa ya fi sarkin ƙarfi, sai ya tuna da gudunsa. Ya yi maza ya sheka a guje, aka yi ta binsa har bayan gari, ba a kama shi ba, aka gaji aka dawo.

Da Idon Matambayi ya gaji da gudu, ya zauna ya huta. Bayan ya huta sai ya manta duk wahalar da ya sha a Kafi, sabo da haka sai wata zuciya ta yi masa shawara ya koma Kafi, watakila Allah ya ba shi wani ɗan abu. Sai ya komo cikin Kafi. Da isarsa sai ya buɗe kyauren wani ƙofar gida ya shiga, ya tafi wani ɗaki a cikin gidan ya iske shi ba kyaure sai tufaniya. Ya ɗauke tufaniyar, ya shiga ɗakin, ya tsaya jikin shamaki ya daɗe. Aka jima kaɗan sai ya nufi sako.

Mai ɗaki ya ce, "Kai wane ne?"

Da Idon Matambayi ya ji haka sai ya yi lif kamar ruwa ya ci shi. Daga nan kuma mai ɗaki ya koma ya yi ta barci yana masori. Idon Matambayi ya tsaya ya daɗe ba motsi, har ya tabbata mai ɗaki yana barci. Ya ɗauki ashana ya kyarta, bai ga kome ba. Ya sake

ƙyartawa, sai ya hangi wata rahoniya, ya je wurinta ya buɗe ta, ya iske babu kome cikinta sai 'yar jaka. Ya ɗauki jakar sai ya ji ƙarar kuɗi. Da jin haka ya yi ta murna yana cewa a zuciyarsa, "Allah na gode ma, tun da ka sa na fita kunyar 'yanuwana!"

Yana cikin fitowa sai ya ji an kama shi da kokawa a ƙofar ɗaki, ana cewa, "'Barawo! 'Barawo!" Har mai ɗaki ya ji ya farka. Ya yi ta kokawa da mutane biyu, har Allah ya ba shi sa'a ya ka da ɗaya. Da ya ka da shi sai ɗayan ya razana, amma Idon Matambayi bai yi masa kome ba, sai ya yi ta kansa, don kada a tarar masa a kama shi. Ya yi ta gudu da takobi a zare. Duk wanda ya gamu da shi, sai ya kai masa sara. Da mutum ya ga an kai masa sara sai ya noƙe, ya yi ta kansa. Haka fa ya yi ta yi a cikin Kafi, har ya tsira.

Da gari ya waye mutanen Kafi duk suka damu sabo da mutuwar Sani da 'yan gadinsa guda huɗu. Sun sani dukan abubuwa na wajen sata Sani ne mai hana su, to, ga shi yau an kashe shi. "Ina za mu sa kammu?" In ji su.

Bayan da aka rufe su Sani, sarkin Kafi ya sa aka tara manyan gari, ya ce, "Kun gani da dukan al'amarin sata da na kisan kai na ɗora shi a kan Sani, to, yau ga shi ya mutu, yaya za mu yi mu zauna lafiya a Kafi? Akwai wani wanda zai raba mu da wannan sharri a garin nan?"

Manyan gari suka yi shiru. Can wani ya ce, "Ranka ya daɗe, yanzu abin da za mu yi sai ka sa a yi shela, dukan wanda ya sani da shi ɗam farauta ne ya zo, da kuma tsohon mayaƙi. Idan sun zo mu hau dawaki mu bi hanyar dutsen Sauke-mu-raba, inda Sani ya ce wata-kila suna nan, tun bai mutu ba."

Sarki ya sa aka yi shela. Kashegari mutane suka taru ƙofar gidan sarki, kowa da bakuna da kibiyoyi da masu.

Sarki Ya Tura Mutane Su Je Neman Ɓarayi

DA isar Idon Matambayi gida sai ya iske 'yanuwansa suna cin abinci da sassafe. Suka ce masa, "Barka, barka da zuwa!"

"Barka kadai."

Ya zauna ya ci abinci tare da su. Da suka gama, Batsokana ya ce, "Idon Matambayi, ina labari?"

"Sai alheri."

Ya nuna musu jakarsa, suka buɗe suka ɓidaya kuɗinta fam huɗu ne da 'yan kai. Idon Matambayi ya faɗa musu dukan irin abin da ya yi a Kafi.

Batsokana ya ce, "Wallahi, rabona da in ga yaro da jan halin Idon Matambayi yau shekara ta yi ashirin. Bayan jan hali ga shi da taurin zuciya, babban abin da a ke so ko wane garnannen ɓarawo ya samu! Da ma abin da ya dame ni abu ɗaya ne, to, ga shi yau an kashe shi. Yanzu ba abin da zai hana mu sata gidan Musa. Mu yi shiri mu tafi."

Yayin da mutanen Kafi suka ji shelar sarki, kowa da sassafe ya yi ɗamara ya yi shiri ya tafi ɓofar gidan sarki. Kafin ɗan hantsi ɓofar gidan sarki ya cika da mutane kamar wurin yaƙi. Sarki ya ce, "Yau ina so ku tafi dutsen Sauke-mu-raba, ku gani ko akwai ɓarayi. In kun same su ku kamo su, in yayyanka su gobe." Mutane suka yi murna da maganar sarki, suka hau dawaki suka tafi.

Yadda muka ce ɗazun, taron ɓarayin nan ba su taɓa yin murna irin ta dawowar Idon Matambayi ba. Ba don kome ba kuwa don ya kashe musu Sani, wanda da su ke shayi. Amma ba su sami labarin zuwan mutanen ba, domin ba su yi zaton akwai wanda zai gane su ba. Suna cikin nashaɗi sai Batsokana ya ce, "Kai, ina jin motsin kamar mutum!"

Ɗauke ya ce, "Haba! Wane mutum ne zai zo nan im

ba wanda muka kawo ba. Kai dai watakila motsin ganyen ka ji. Amma bari in je in hango."

Da fitowarsa sai ya hango mutane ɗakaka suna tafe, waɗansu a kan dawaki, waɗansu kuwa a ƙafa. Ya yi maza ya zo ya gaya wa 'yanuwansa. Batsokana ya ce, "To, yau ina za mu saka kammu? Da ma na yi zaton haka, am biyo mu ne a kame mu, duk a kashe mu."

Idon Matambayi ya ce, "Ina yadda za mu yi? Gama dai sun zo kusa yanzu, balle mu guje musu."

Batsokana ya ce, "Da dai akwai wani ɗan wuri a nan, da sai mu ɓoye, to, babu."

'Dauke ya ce, "Akwai mana! Ina wurin da muka gina kwanan baya sabo da dukiyar fashi?"

Kwace ya ce, "Yana nan, ya kuwa ishe mu!"

Kafin mutanen Kafi su iso suka yi maza-maza suka ɗuru cikin ramin nan. Mutanen nan da suka iso suka shiga cikin dutsen Sauke-mu-raba, suka iske babu kowa.

Wani ya ce, "Ai babu kowa a gidan."

Wani ya ce, "To, ina suka yi?"

Suka yi ta nema suka yi ta nema, har Allah ya gajishe su, ba su ga kowa ba. Su leƙa nan, su duba nan, ba su ga kowa ba. Da suka gaji da nema sai suka koma Kafi, suka faɗa wa sarki ba su ga kowa ba. Sarki ya ce, "In ce ko kun ga alamar wurin da mutane?"

Suka ce, "Nan su ke, amma ba su a gidan lokaçin da muka je." Sarki ya ce, "Kowa ya tafi gida ya huta sai jibi, kowa ya yi shiri a koma ko a same su. Daga yanzu kuma duk baƙon da aka gani kada ko wane mai gida ya sauke shi, kome samunsa." Da sarki ya gama zancensa, mutane suka kama hanya suka koma gidajensu.

Bayan da mutane suka tafi su Batsokana suka fito daga rami, suka zauna suna shawara. Idon Matambayi ya ce, "Tun da aka rigaya aka gane mu ya kamata mu sake wuri, im ba haka ba kuwa ma ga yadda ba ma so."

'Yanuwansa suka yarda. Suka yi ta jidon kayansu suka koma wani kogon dutse nesa daga dutsen Sauke-mu-raba. Wuri ne kuwa mai ni'ima ƙwarai.

Idon Matambayi ya ce, "Yaya za a yi, a yi wa Musa sata?"

Batsokana ya ce, "Bari tukuna sai mutanen Kafi sun soma mantawa da mu."

Da ya ce haka sauran ɓarayin suka riƙa zaton watakila Batsokana yana jin tsoro ne, sabo da haka Kwace ya yi farat ya ce, "Mu bari! Mu bar me? To, har yaushe? In dai wajen mutanen Kafi ne, wallahi, ba za su manta da mu ba har abada. Ku duba abin da'Dauke ya yi, da abin da Idon Matambayi ma ya yi. Yaya! Yaya za su manta mu? Kai, im ba mu tafi tun da wuri ba, wallahi, a gane mu a zo duk a kame mu! Wa ya san abin da Allah zai yi gobe?"

Da Kwace ya gama maganar sai Batsokana ya tambayi 'Dauke da Idon Matambayi ya ce, "To, me kuka gani, kun ji abin da Kwace ya ce?"

Suka ce, "A'a! Me za mu ce? Gani na gare ka. Mu dai mun yi mai wuyar tun da muka cika alkawarimmu, muka yi kuwa abin da ka faɗa mana."

Batsokana ya farga cewa dukan 'yanuwansa ba abin da su ke so sai su tafi Kafi a yi wa Musa sata. In ya ƙi kuwa watakila sai su halaka shi. Sabo da haka ya ce, "In Allah ya yarda gobe-goben nan ma tafi, mu washe Musa."

Sun Kai Hari Gidan Musa

DA rana ta zo wace sarkin Kafi ya ce da mutanensa za su koma dutsen Sauke-mu-raba sai kowa ya yi shiri ya zo ƙofar gidan sarki. Da suka haɗu kaf sai suka ɗunguma suka tafi. Da isarsu suka iske babu kowa a can suka dawo suka ba sarki labari.

Sarki ya ce, "Barayin sun tsorata, kowa ya koma gida ya saki jikinsa."

Da gari ya waye Batsokana ya ce, "To, abin da za mu yi yanzu sai mu yi shiga irin ta 'yan kasuwa, mu tafi har gidan Musa, mu ce goro muka zo saye. Ni zan zama shugabanku, in ce ku barorina ne. Amma fa kada ku manta ku tafi da makamai iri iri, da kuɗi ƒam hamsin na sayen goro, domin ba mu san yadda za mu sami gidan ba." Suka ce, "To."



Suka kama hanya suka tafi, ba su isa Kafi ba sai bayan azahar, domin ba su fita gida da wuri ba. Da shigarsu garin, suka yi ta tambaya kamar waɗanda ba su taɓa zuwa ba, har wani mutum ya nuna musu gidan Musa. Da zuwansu, sai suka iske gida cike da barori madaka kuka, suna ta ƙidayar goro, waɗansu kuwa suna ta ɗaurin fata da ƙirgi. Da shigarsu suka gaisa da wani mutum, suka ce masa sun zo wurin Musa ne. Mutumin nan ya faɗa wa Musa, Musa ya ce su shigo.

Batsokana ya ce wa 'yanuwansa, "Ku dakata."

Da shigar Batsokana ya iske Musa zaune a kan mawanka, mutane kuwa suna kewaye da shi. Batsokana ya kwanta, suka gaisa da Musa, ya ce ya zo sayen goro ne, da shi da yaransa guda uku. Musa ya ce, "A kira yaran in gan su."

Aka kira su, suka shiga suka zauna. Musa ya ce, "Sannu sannunku, samari. Muna lafiya ? Yaya gida ?"

Suka ce, "Lafiya lau!"

Aka daɗe Batsokana ya ce da Musa, "Ba ka fa shaida ni ba ?"

Musa ya ce, "A'a."

Batsokana ya ce, "Ai ni ne Ibrahim abokin Hassan na Jibiya, abokinka. Bara waccan mun zo da shi wurinka."

Musa kuwa yana da aboki Hassan a Jibiya, sabo da haka da ya ji maganar Batsokana, sai ya yi zaton gaskiya ce. Musa ya yi tunani ya gane Ibrahim bai gane shi ba, amma ya sani lalle Hassan na Jibiya ya zo wurinsa bara waccan. Ya ce, "Ashe yau ba baƙi ke gare ni ba, abokai ne. Ai waɗannan ba a kai su masauki ba, ni ne zan sauke su." Ya sa aka ba su ɗaki a shamakin gidansa. Da almuru ta yi aka kawo musu abinci da toye-toyen daɗi.

Bayan sun ci sun ƙoshi sun soma hirar abin da za su yi idan dare ya yi, Batsokana ya ce, "Kun ga wani abu dai?"

"A'a, ba mu lura da kome ba har yanzu!"

Batsokana ya ce, "Ya kamata kuwa mu san wacce mu ke ciki kafin dare ya yi sosai."

Idon Matambayi ya ce, "Yau ba abin da za mu yi. Mu bari sai gobe, ido na ganin ido, mun ga kome."

Ɗauke ya ce, "Kada fa mu zauna har a gane mu."

Idon Matambayi ya ce, "Haba! Ai ƙarya da dabara ba su ƙarewa a wurimmu."

Shawararsu ta haɗu daidai ba za su yi sata ba sai gobe. Ashe duk abin da su ke cewa wani yaron Musa yana laɓe yana ji, sabo da haka da wayewar gari sai ya tafi wurin Musa, ya iske shi tare da su Batsokana suna zance. Ya ce wa Musa, "Maigida, ina so mu gana."

Musa ya tashi suka tafi waje ɗaya suka zauna, yaron ya ce, "Allah ya bar maigida, abin da ya sa na ce mu gana domin im faɗa maka jiya da almuru na ji baƙinka suna niyyar yi maka sata. Musa ya yi ta mamaki yana cewa, "Ɓarayi! Ɓarayi! Waɗanne irin ɓarayi?" Suka gama zance suka fito.

Da Musa ya koma wurin zamansa na da, sai su Batsokana suka ga fuskarsa ta sake. Aka jima kaɗan Batsokana ya ce, "Muna so a fito mana da goro mu duba mu saya."

Musa ya ce, "Yaushe za ku tashi?"

"Im muka sayi goron yau, muka shirya shi, gobe kuma sai gida."

"Allah ya kai mu goben!"

Musa ya sa babban baransa ya zaga da Batsokana da 'yanuwansa wurin kwandunan goro don su ga wanda zai yi musu. Yayin da duk su ke zagawan nan ko wanensu yana duba wuri wuri a cikin gidan. Bayan

sun gama yawonsu suka zo suka ce da Musa sun ga irin goron da su ke so. Musa ya faɗa musu kuɗin ko wace ƙwarya. Suka ɗebi kuɗi fam hamsin suka biya, suka wuni shisshirya goronsu suka ɗaure a huhu huhu. Da Musa ya ga yadda suka sayi goron nan sai ya yi ta murna, yana kuma mamakin abin da yaronsa ya faɗa masa. Ya tuna tsakaninsa da Hassan na Jibiya babu munafunci. Sabo da haka bai ƙara tunawa da maganar yaronsa ba.

Da almuru ta yi, aka kai wa su Batsokana abinci kamar jiya, suka ci suka ƙoshi. Batsokana ya tambayi 'yanuwansa ya ce, "Ina dabara?"

Suka ce, "Dabara na wurinka."

Batsokana ya ce, "Ko Allah ya sa wani a cikinku ya nakalci abin da baran Musa ya faɗa masa da suka gana?"

"A'a, ba mu sani ba."

"Ina zato watakila jiya ya ji abin da mu ke cewa da dare. Ba ku ga da Musa ya komo ba fuskarsa ta yi murtuk?"

Shiru ba su amsa ba, sa'an nan suka ce, "To, ai Allah ne mai yin kome."

Labarin nan da Batsokana ya faɗa wa 'yanuwansa shi ne dalilin rabuwarsu, gama da suka ji haka sai suka yi ta tsammanin Batsokana ba ya da wata dabara ɗa zai nuna musu, balle su yi sata. Sabo da haka da ya tafi ya gaida Musa da dare sai Kwace ya ce, "Wallahi, im ba mu yi hankali ba, Batsokana zai wahalshe mu a banza."

Idon Matambayi ya kada baki ya ce, "Ni ma dai na soma ƙin Batsokana. Sau da yawa ke nan ya ke wahalshe mu. In ka tona watakila ba don kome ya sa ya ke zaune da mu ba, sai don mu je yin sata a kashe mu ya ɗebe dukiyarmu."

'Dauke ya ce, "Hakanan ne, Batsokana ba ya da kome sai ruba, mu dai mun rigaya mun karai da shi ne tun da muka gamu da shi."

Yayin da duk su ke zancen nan Batsokana yana tare da Musa suna zance, yana yi masa 'yan tambayoyi. Da kowa a cikinsu ya ƙare zancensa sai Idon Matambayi ya sake cewa, "Abin da na gani ya fiye mana yau da dare mu tashi, ko mu yi sata ko mu yi tafiyarmu gida, gama Batsokana zaunad da mu zai yi a garin nan, har a gane mu a kama mu."

'Dauke ya ce, "Watakila ma a kashe mu duk."

Suka yarda da shawarar Idon Matambayi kafin Batsokana ya komo. Da ya komo ya ce musu, "Tun da ya ke ba mu sami damar ganin gidan nan ba sosai ya kamata mu daɗa wani kwanan. Ko ba haka ba?"

Suka ce, "Sosai!" Don kada ya gane dabararsu.

Aka jima kaɗan suka kwanta suna barci. Can tsakar dare Idon Matambayi ya tashi ya taɓa Kwace a hankali ya farka, ya je ya taɓa 'Dauke shi kuma ya farka. Suka tashi saɗaf, Batsokana yana ta sheƙa barci. Idon Matambayi ya ce musu da raɗa, "Mu ɗauki makamammu duk, mu yi shiri, mu bar goron mu shiga cikin gidan, ko mu yi sata ko a kama mu."

'Dauke ya ce, "Watakila ma a kashe mu duk."

Suka yarda da shawarar Idon Matambayi kafin Batsokana ya komo. Da ya komo ya ce musu, "Tun da ya ke ba mu sami damar ganin gidan nan ba sosai ya kamata mu daɗa wani kwanan. Ko ba haka ba?"

Suka ce, "Sosai!" Don kada ya gane dabararsu.

Aka jima kaɗan suka kwanta suna barci. Can tsakar dare Idon Matambayi ya tashi ya taɓa Kwace a hankali ya farka, ya je ya taɓa 'Dauke shi kuma ya farka. Suka tashi saɗaf, Batsokana yana ta sheƙa barci. Idon Matambayi ya ce musu da raɗa, "Mu ɗauki makamam-

mu duk, mu yi shiri, mu bar goron mu shiga cikin gidan, ko mu yi sata ko a kama mu."

Suka shisshirya sarai suka fita a hankali, suka yi ta zaga gidan nan ko sa ga wata 'yar hanya. Yawon nan duk da su ke yi dugadugansu ba su taɓa ƙasa, don ƙada motsin tafiyarsu ya farkad da Musa ko wani baransa. Suna cikin yawonsu sai Idon Matambayi ya hangi wani abu, ya ce, "Mene ne can sanda-sanda?"

'Dauke ya je ya duba, sai ya iske tsani ne dogo ƙwarai. Idon Matambayi ya ce, "Allah ba yadda ba ya yi! Kun gani mu da kammu muka sami tsani."

Suka ɗauki tsanin nan suka sa shi jikin katanga. Idon Matambayi ya ce, "Mutum biyu su riƙe, ni kuwa in shiga gidan tukun, sa'an nan wani ya biyo ni." Kwace ya tambaya ya ce, "Da ni da kai, ko da kai da 'Dauke?"

Idon Matambayi ya ce, "Bari mu je da 'Dauke kai ka tsaya, ko ba haka ba?"

"To, shi ke nan."

Idon Matambayi ya kama tsani ya hau ɗaf ɗaf, 'Dauke da Kwace suna riƙe, har ya isa bisa katanga ya sa hannu ya tuttumɓuke gauɗen bisanta, ya tsirga ciki. Idon Matambayi da shigansa gidan, sai ya tafi ɗaya soron ƙofar gida, ya iske shi kulle da sakata, ya ja ƙofa ta buɗe, 'Dauke ya shiga gidan, suka yi ta neman ɗakin da za su shiga. Duk ɗakin da suka je sai su iske shi ƙulle da ƙyaure mai ƙwari, ko motsi ba ya yi. Idon Matambayi ya ce, "Ina dundurusu."

'Dauke ya ce, "Yana wurin Kwace."

'Dauke ya tafi ya ɗauko dundurusu wurin Kwace, suka yi ta haƙin ƙyauren wani ɗaki har suka ɗaɗɗake shi ƙalau.

Allah ya ƙaddara a ɗakin nan da suka buɗe kuɗin Musa su ke duk. Ba wanda ko ya ke kwana cikinsa

don Musan ya amince da ƙwarin ƙyauren. Wannan ya zama babban taimako wurin ɓarayin nan, gama lalle ne in da ba mutum cikinsa da ya ji motsinsu lokacin da su ke haƙin ƙofar. To, babu.

Da shigarsu suka yi ta duba nan da can a cikin ɗakin nan, ba su ga kome ba. Suna cikin nema sai Idon Matambayi ya ga wani ɗan gini jikin bango, an shafe shi da jar ƙasa. Ya sa dundurusu ya doki wurin kamar sau uku, sai ya ji motsi kuf kuf, kamar rami'an rufe shi da kasko. Ɗauke ya ce, "Ba shakka, wurin nan ba banza ba."

Idon Matambayi ya daɗa bugar ginin da ƙarfi kaɗan sai gini ya dare, kuɗi suna kwarara. Suka yi ta kwasar kuɗin nan suna kai wa wurin Kwace har suka gaji, suka ƙunƙunshe kuɗin kowa ya ɗauka, suka yi ta tafiya har gidansu. Allah ya sa kuwa ba su gamu da ɗan gadi ba ko guda, domin gari ya kusa wayewa. Kuɗin da suka ɗiba bayan sun ƙidaya suka iske wajen jaka biyar ne.

DUK abin nan da ya faru Batsokana bai sani ba, haka kuma Musa mai gida. Batsokana bai tashi daga barci ba har Musa ya tashi ya yi alwala ya yi salla. Kuma Musa bai lura da ɗakin kuɗinsa ba lokacin da ya fito yin salla. Matarsa ta fito daga ɗaki za ta yi salla, da ta duba wajen ɗakin kuɗi sai ta ga ƙofa a buɗe, ƙyaure yana waje ɗaya. Ta tafi da sauri wurin mijinta ta tambaye shi ta ce, "Maigida, kai ne ka buɗe ƙofar ɗakin kuɗi, ka bar ta a buɗe?"

Da Musa ya ji haka sai cikinsa ya ce ƙululu. Ya tafi da sauri ya shiga ɗaki ya iske ginin da kuɗi su ke ciki a fashe, kuɗi barjat a cikin ɗakin. A lokacin nan shi da kansa bai san iyakacin kuɗin da aka ɗiba ba.

Ya yi salati, ya sanad da Ubangiji ya ce, "Watau maganar da yarona ya ce mini ta tabbata! Ashe dai baƙin nan nawa ɓarayi ne!"

Daga ɗakin nan da ya fita bai zame ba sai ɗakin da ya sauki Batsokana da 'yanuwansa. Da ya je ya iske Batsokana yana ta barci, huhunan goro kuwa suna waje ɗaya. Bai tashe shi ba sai da ya tashi barorin gidansa duk, ya ce su tare ƙofar gida. Ya ɗebi ƙatta biyar daga cikin yaransa, ya koma da su ɗakin Batsokana. Da isarsu suka tashe shi. Da ya tashi sai suka rufe shi da duka har ya faɗi sumamme. Da ya farka aka yi masa ƙuƙumi, aka tafi da shi gidan sarkin Kafi.

Batsokana ya yi mamaki yana cewa a zuciyarsa, "M mhm! Ni Batsokana na yi wa kaina, mutanen nan 'Dauke da Kwace da Idon Matambayi sun kyauta. Suka zo suka yi sata suka tafi suka bar ni. Amma da ikon Allah sai mun haɗu, ko ba daɗe ko ba jima."

Da sarki ya fito wurin shari'a aka kawo Batsokana da Musa. Musa ya ba da labarin yadda Batsokana ya yi, da shi da 'yanuwansa, ya kuma faɗi abin da baransa ya faɗa masa game da su.

Sarki ya ce wa malamansa, "Jama'a, me kuka gani?"

Malamai suka ce, "Shi wannan mutum ba su kama shi da kayan sata ba. To, yaya fa za a ɗaure mutum babu kayan sata? Daɗin daɗawa kuma ka tuna ka yi dokar cewa kada kowa ya sauki baƙo ba da izninka ba, yaya Musa zai sauki baƙo da kansa, ya komo ya ce baƙon nan ya yi masa sata?"

Sarki ya ce, "Na ji."

Aka yi waiwaye ga Batsokana, Batsokana ya ce a marairaice yana tattausa muryarsa kamar wani wanda aka zalunta, cewa, "Ran sarki ya daɗe, ni mutumin Jibiya ne, na zo da kuɗina don in sayi goro. Na daɗe da sanin garin nan. Na daɗe kuma da sanin Musa."

Musa ya ce, "Ni ban san ka ba!"

Mutane suka ce, "Shiru! Kada ka yi surutu!"

"Dalilin sabawarmu kuwa wani abokina wai shi Hassan. Shi ya hada mu da Musa, muka shaku kwarai. Sabo da sabawan nan har ba ya kan sauke ni a wani gida ba sai a gidansa. Mutanen kuwa da ya fada ban san su ba, karya ya ke mini. Ranar da na zo ya hada ni kwana da baki mutum uku. Da gari ya waye ina cikin barci sai ya tashe ni ya sa aka yi ta mini duka har na suma. Da na farko ya daure ni ya kawo ni wurin nan."

Sarki da malamansa suka ce, "Ka ji, Musa, abin da wannan ya ce?"

Musa ya ce, "Karya ya ke, shi ya zo da haukan nan."

Sarki ya ce, "Tashi ka fita, yaya za ka amince wa mutum, kana ka zo ka ce da shi ɓarawo? Ko ba ka san Hassan din da wannan ya fadi ba a Jihiya?"

Musa ya ce, "Ranka ya dade, na san shi."

Sarki ya ce, "Abin da ya sa ka san Hassan shi zai sa ka san mutumin nan. Tashi, ka ba ni wuri! Kai kuwa wannan mutum ka rantse ba ka yi wa Musa sata ba?"

Batsokana ya ce, "Na rantse."

Aka ba Batsokana ruwa, ya je ya yi alwalla ya rantse, aka sake shi.

Batsokana Ya Iske Sauran Barayin

BAYAN da su Idon Matambayi suka ƙare ƙidayar kuɗinsu suna murna, sai suka ci abinci, suka koma waje ɗaya suka zauna suna dararraku.

Idon Matambyi ya ce, "To, yau bukatarmu ta biya. Abin da ya fiye mana mu ɗebo dukiyarmu da kuɗimmu duk waɗanda muka tara mu ga yawansu. Im mun gani mu raba daidai, mu rabu da wurin nan. Ba mu sani ba ko in an kama Batsokana zai tona asirimmu. Ni da ma abin da na ke so a cikin sha'anin sata, in sami dukiya da kuɗi masu yawa. Ga shi kuwa yau mun samu. Na tabbata im mun zauna wurin nan wata rana za mu halaka. Batsokana da kuka gan shi ba mutumin da za mu zauna da shi ba ne, gama abin da ya ke so ya zauna wuri ɗaya mutane su je su kawo masa dukiya. Ba don mun farga da shi ba da wuri, wallahi, da da kyar za mu fito Kafi ba a kama wanimmu ba. Na gode Allahu da ya hada ni da ku, kuka riƙa bin shawarata, ina bin taku."

Da ya gama maganarsa, 'Dauke da Kwace suka yi shiru kaɗan. Can 'Dauke ya ce, "Allah mun gode maka tun da ka biya mana bukatarmu. Ba don wani abu ne ya sa muka sami dukiyan nan ba, sai don bakimmu ya zo ɗaya. Kun ga da bakimmu bai zo ɗaya da Batsokana ba ga yadda muka yi masa. Allah ya bar aminci a tsakanimmu. Amma dai ga zancen barin sata da ka ce, ni tun ina yaro da ita na buɗe ido, cikin dukan sana'o'i ban san ko ɗaya ba. Ka kuwa sani mai hali ba ya bari, ko na ce na bar sata, ƙarya na ke yi. Saura Kwace me ka gani?"

Kwace ya ce, "Ni ma na gode Allah, na ko gode muku tun da ya ke ko yaushe na tashi ɓata mana shirimmu ku kan hana ni, ni kuwa ba ni kan yi fushi ba don kun hana ni. Amma bisa maganar da ka faɗi, da ni da 'Dauke

kamar ciki ɗaya muka fito, ba ni da wata shawara sai abin da ya ce. Amma idan Idon Matambayi ya tsaya a kan barin sata, sai a raba a ba shi nasa rabo, ya yi tafiyarsa, mu kuwa muna nan tare."

Idon Matambayi ya ce, "Ni dai ina nan bisa maganata. In kun bi tawa kuwa rabuwarmu da wurin nan ita ce alheri, tun da ya ke Allah ya ba mu sa'a. Amma im ba haka ba kun ga tafiyata. Allah ya ba mu lafiya." Aka yi rabo ya kwashi nasa ya tafi.

Ba a jima ba sai suka ji dudduge, suka leƙa, ashe Batsokana ne ya zo. Da ganinsa suka dubi juna, kunya ta ishe su, suka rasa abin da za su ce masa.



Batsokana ya zauna ya ce, "Haba, 'Dauke, don me kuka ba ni kunya, sai ka ce ba ɓarayi ba?"

Suka yi shiru, can Kwace ya ce, "Abin da ya sa muka

yi maka haka, mun ga ba ka da niyyar sata. Ai da mun bi taka, har yanzu da muna can muna zaman banza."

Batsokana ya ce, "Ku dai halinku na yara ke nan. Ai ko da na sani ba ku isa shawara ba, ba ku kuma yarda da ni ba, shi ne ya sa ban buɗe muku asirin gidan Musa ba."

Suka ce, "Ai mu ma mun buɗe asirin da kammu, ba da taimakonka ba."

Batsokana ya ce, "Me kuka ɗiba? Kananan ɓarayi kurum, me ya raba ku da 'yan sane?"

Sai suka yi fushi suka ce, "Zo ka gani."

Suka tafi da shi ya gani. Ya ce, "Dan abin ke nan? Ina saura?"

Sai 'Dauke ya tasam masa kamar zai buge shi.

Batsokana ya ce, "Ai ba maganar faɗa ba ce, mu je mu zauna, in gaya muku." Ya ce, "Watakila kun yi tsammani ba za ku ƙara ganina ba, tun da kuka yi sata kuka bar ni a gidan Musa. Amma abin da ya sa ba a kama ni ba, na tashi da dare na ga ba ku nan, na fita waje garin duban abin da ya faru, har na zo ɗakin da kuka haƙa, na ga abin da kuka yi, na maida ƙyaure, na ɓad da sawu da kaina don kada a gane."

Suka ce, "Ina amfanin wannan, tun da muka rigaya muka sami abin?"

Batsokana ya ce, "Bari in gaya muku. Kuna tsammani attajiri kamar Musa zai ajiye dukiyarsa a ɗan ɗaki irin wannan?" Suka ce, "To, kai, me ka gani?"

Batsokana ya ce musu, "Kun sani na san gidan nan tun da, jinkirin da na yi kuwa don in tabbatad da abin da na sani ne kana in gaya muku. Na tabbata sosai ke nan, na gama shirya dabarata da yadda za mu samu. Ina shirin in gaya muku, sai kuka zo kuka yi mini wannan rashin hankali, kuna neman ku ɓata mini dabarata.

Suka ce, "Me ka tabbata?"

Batsokana ya ce, "Daga dai-dai nan da kuka shiga, in kun yi arewa akwai wata babbar tuduwar tsiya, nan ainihin dukiyar ta ke. Amma ya kamata ku bi bakin ta yadda ba za a gane ba, sai kamar ni da na ke da wankin ido."

Sai suka dubi juna sai suka ce, "Ashe akwai wata dukiya ban da wadda muka samu?"

Ya ce, "Kai, ina ga ku da kiwon awaki, kuna kyalla ta haihu." Abin da kuka samu ko ushiri ya yi?"

Suka ce, "To, ina dabara?"

Ya ce, "Akwai dabara, amma ni ban yarda da ku ba. Wa ya sani ko in na tafi da ku za ku sake yi mini irin ta da? Gwamma in nemi wadansu, wadanda za su tsaya a kan maganata."

Sai K'waee ya ce, "Haba Batsokana, babba ba ya fushi. Ma bu ka Da ma ya kamata ka sani ba mu ne muka yi maka haka ba, da mu ne da ba za ka tarad da mu a nan ba. Yaron nan Idon Matambayi shi ya kuta mana."

Batsokana ya ce, "Ina ya ke yanzu?"

'Dauke ya ce, "Ai ko da mu da shi gamuwar hanya ce. Ya tafi abinsa. Watakila don kunyar kada ku hadaido ne."

Batsokana ya ce, "Dam banza! Ai ko da kun dakata mini mun yi wannan tare, nufina mu rabu da shi."

Suka ce, "Shi ma ya gaya mana talauci kadai ya sa shi yin sata."

Batsokana ya ce "To, shi ke nan, mun rabu da shi. To, yanzu na yafe muku, amma in kuma so mu yi wannan abu tare, sai ku tausa za ku yi dukan abin da na gaya muku."

Suka ce sun ji. Can ba, suka tausa.

Ya ce, "Yanzu ku sami Musa bai waye an yi masa

sata ba tukuna, sai mu gaggauta mu koma tun bai gane ba."

Suka ce, "Ai ko yau sai mu je."

Da dare ya yi suka yi shiri suka fito, suka shiga cikin Kafi suna bi lungu-lungu har suka kai gidan Musa.

Sai Batsokana ya ce, "Ku tsaya nan, in nemo tsani."

Sai ya tafi, bai jima ba sai ga shi ɗauke da wani dogon tsani, ya ce, "To, ku ɗauka mu je mu dangana daga arewa, domin nan rijiyar ta ke."

Suka ɗauka suka kai suka dangana inda ya nuna musu. Suka hau suka ɓaɓɓalle gauɗe suka shiga. Ya wuce gaba suna biye da shi. Suka yi 'yar tafiya kaɗan sai ya duƙa kamar yana neman wani abu, yana lalabe suna kallonsa, sai suka ji ya ce, "Madalla! Ga wurin."

Ya ce, "Mu fara tonawa da wuƙaƙemmu."

Suka taɓa kaɗan, 'Dauke ya ce, "Kai, wurin da ƙarfi!"

Batsokana ya ce, "Ai kuwa inda na ɗauko tsanin nan na ga dundurusu da dagi. Ba nisa. Ku maƙe, in tafi yanzu in kawo su."

Ya zo ya taka tsani ya hau ya jawo ya sa a waje ya sauka, ya tafi a guje, bai zame ba sai gidan muƙaddashin 'yan gadi. Da zuwa ya bugi ƙofa, aka ce, "Wane ne?"

Ya ce, "Barayi ne na gani sun sa tsani sun shiga gidan Musa.

Aka je aka taso muƙaddas. Da ya ji nan da nan ya tara 'yan gadi. Batsokana ya ce, "Ku biyo ni, kada ku yi hayaniya."

Ya kawo su, ya ce, "Ga inda na gan su."

Sai suka yi wa gidan ƙawanya, sa'an nan muƙadda ya bugi ƙofar gida, aka buɗe. Ya ce, "Kai, akwai ɓaraya gidan nan."

Mai gida ya kunna fitila, suka shiga. Suna shig muƙaddas ya hange su, ya ce, "Ga su can! Maza k

kama! Nan da nan aka cafke su, aka nufi da su gidan yari.

Amma Batsokana da ganin an kewaye gida bai tsaya ba, sai ya koma gida da hanzari, ya shiga, ya ɗebe dukiyar sarai, ya tafi.

Da gari ya waye, aka zo da su gaban sarki tare da Musa. Musa ya shaida ya ce, "Su ne suka zo gidana tare da muƙurnin da muka yi shari'a da shi jiya. Su suka yi mini sata."

Aka yi ta tuhumarsu har aka tabbata dukan satar da aka yi a gari su suka yi, har aka ce su ne suka kashe sarkin gadi. Amma wannan bai tabbata ba.

Sarki ya ce, "Kuna da magana?"

Da suka ga ba su da hanyar fita, kuma suka gane dukan wannan kissar Batsokana ce, suka ce, "Ranka ya daɗe, yaya za a bar jaki a riƙa bugun taiki? Mu dai dukan abin nan sa mu aka yi."

Sarki ya ce, "Wa ya sa ku?"

Suka ce, "Wanda aka kama gidan Musa shekaranjiya."

Sarki ya ce, "Ashe!"

Suka ce, "I, ko yanzu kuwa shi ya sake kawo mu."

Sarki ya ce, "Yana ina?"

Suka gaya masa yadda ya rabu da su.

Sai mukaddashin 'yan gadi ya ce, "Ko shi ne ya zo ya ta da ni jiya da dare, mai kama kaza?"

Sarki ya ce, "Shi ne lalle. Me ya sa ya yi muku haka?"

Suka ce, "Domin ran nan tare muka tafi gidan Musa garin sata, amma muka yi masa dabara, mu muka sami dukiya, shi kuwa aka kama shi. Shi ya sa ya rama, don ya zaga ya kwashe."

Sarki ya ce, "Idan haka ne in kun faɗa mini gaskiya inda za a same shi duk da dukiyan nan, na yi muku rangwame."

Suka faɗa masa, ya sa aka tafi wurin. Aka iske wa-

ɗansu tufafi, amma babu ƙarfe, babu Batsokana. Aka yi ta nemansa, amma ba a ƙara jin ɗuriyarsa ba. Su kuma aka ɗiba musu odar shekara bakwai bakwai.

Idon Matambayi Ya Tuba Da Sata

RANAR da Idon Matambayi ya shiga garinsu ya iske ubansa ya mutu. Kashegari sarki ya sa aka kama shi aka ɗaure har kwana uku. Aka kawo shi gaban sarki, sarki ya ce, "Kai, im ba ka bar sata ba, zan ɗaure ka rai da rai."

Idon Matambayi ya ce, "Ranka ya daɗe, kada ka yi zancen ɗauri rai da rai, kai dai ka ce in tuba, na kuwa tuban. Da ma don na tuban ne shi ya sa ka ga na komo garin nan. In kana shakka ka sa a kawo mini Alƙur'ani in rantse, ba zan ƙara sata ba."

Da sarki ya ji batun nan sai ya hana Idon Matambayi rantsuwa, ya ce dukan taron mutanen wurin nan su sa wa Idon Matambayi albarka sabo da ya bar sata, su yi wa ubansa addu'a Allah ya ji ƙansa.

Idon Matambayi ya koma gidansu ya yi ta jin daɗi. Bai yi wata guda da zuwa ba sai gobara ta tashi a kusa da gidansu da rana kata, ta ƙone gidan maƙwabtan da na su Idon Matambayi, kayansa suka ƙone, kuɗinsa suka lalace, ya koma ba wuri ba wurin zama.